**COURSE GUIDE**

# HAU 105
# GABATAR DA ADABIN HAUSA (INTRODUCTION TO HAUSA LITERATURE)

**Course Team:** Dr. Aliyu Isa Sulaiman (Course Writer) - Kaduna State University, Kaduna.
Professor Ibrahim Malumfashi (Course Editor) - Kaduna State University, Kaduna.

NOUN

**NATIONAL OPEN UNIßERSITY OF NIGERIA**

@ 2023 by NOUN Press
National Open Uniϐersity of Nigeria
Headƙuarters
Uniϐersity Ɓillage
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Edƥressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Ɓictoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Published by:
National Open University of Nigeria

Printed: 2023

ISBN: 978-978-058-845-8

**HAU105: Gabatar Da Adabin Hausa (Introduction to Hausa Literature) 2CU**

**Gabatarwa (Introduction**)
Darasin HAU105, yana ɗaya daga cikin darussan da ya kamata a karanta ga wanda ke nazarin harshen Hausa, kwas ne da ke magana kan adabin Hausa. Bayanan dake cikin wannan manhaja suna gabatar da wannan darasi ne tun daga ma'ana ita kanta kalmar adabi da rabe-rabensa. Haka nan kuma an yi bayanin dangantaka da ke tsakanin adabi da al'ada, wadda ta nuna tamkar tsoka ce da jini wanda suke rayuwa da juna. Wannan manhanja tana bayani kan abin da kwas ya ƙunsa da kuma abubuwan da kwas yake bukata da yadda ake iya tsamo abin da ake bukata a cikin abubuwan al'ada da cinikayya da shugabanci. Manhajar na bayanin irin abubuwan da suka kamata ga ɗalibi ya kiyaye a yayin da yake nazarta kowane kashi. Haka nan kuma, manhajar ta kawo tambayoyi waɗanda ake bukatar mai nazari ya amsa, don yin haka zai taimaka wajen fahimtar abin da kwas din yake koyarwa. Yana da kyau idan an sami matsololi ko rashin fahimtar wani kashi ko darasi a garzaya faɗin haka a yayin tattaunawa da malaman da ke kula ko koyar da wannan darasin. Ya zama wajibi a rinƙa tuntubar malami ko malamai kan wasu abubuwan da suka shigewa ɗalibai duhu a yayin da ake tattaunawa tsakanin malamai da ɗalibai (tutorial class). Yin haka zai taimaka ainun wurin samun nasarar isar da sako ga ɗalibi.

**Manufar Wannan Kwas (Course Aim)**
A kowane kashi, akwai muhimman abubuwa da ake fata ɗalibai su sani game da wannan kashi, wato manufar da ake ƙoƙarin a cimmawa yayin da aka kammala karatun wannan kashin. Don haka, a karanta manufar da kyau a kuma fahimce ta sosai da sosai. Da zarar an san manufar da wannan kashi ko darasi take fatar ta cimma wa, to ɗalibai za su iya gwada ƙimar ganewarsu ko rashin gane darasin da suka karanta.
A taƙaice, wannnan darasi na gabatar da adabin Hausa (HAU105) ne, akwai muhimman manufofin da wannan darasi yake ƙoƙarin isar wa ga mai karatu waɗanda suka haɗa da:

- Ma'ana da ire-iren adabi
- Banbancin adabi da al'ada da kuma muhimmanci adabi ga rayuwar Bahaushe
- Ma'ana da ire-iren adabin gargajiya
- Ma'ana da ire-iren adabin zamani

**Koyo Tsantsa (Working Through the Course)**
Samun nasarar kammala wannan kwas ya rataya ne kan nazartar kowane kashi a tsanake tare da bibbiyar manazaratar da aka gabatar domin ƙarin haske da samun ƙarin bayanai. Haka nan kuma kada a shagala da duba wasu abubuwan ƙara nazari da NOUN ta tanadarwa ɗalibai domin inganta karatunsu da kaifafa fahimtar abin da aka sa wa gaba. A ƙarshen

kowane kashi, akwai tambayoyi, su waɗannan tambayoyin an yi su ne domin su auna fahimtar mai karatu dangane da abin da ya karanta. Haka nan kuma akwai JINGA (Tutor Marked Assignment) waɗanda aka tsara domin ɗalibai. Ana bukatar idan an amsa waɗannan tambayoyi, to a miƙa amsoshin ga malaman da ke kula da darasin domin a duba a kuma bayar da sakamakon da ya cancanta. Su waɗannan ayyuka na "Jinga" da aka ba ɗalibai suna taimakawa wajer harhaɗa sakamakon jarabawar ƙarshen zangon karatu domin fitar da sakamakon kowane kwas da ɗalibai suka yi. Wannan kwas yana da Rukuni guda Uku, a kowane rukuni akwai kashi biyar, saboda haka ana sa ran ɗalibai su kammala wannan kwas cikin satuttuka goma sha biyar zuwa sha bakwai, kowane rukuni yana da alaƙa da mai bi masa, haka nan kowane kashi yana da dangantaka da mai biye da shi. Saboda haka, kada ɗalibai su tsallake wani kashi zuwa wani kashi, yin haka kan gungurta fahimta da rashin gane abin da kwas yake koyarwa.

Ana shawartar kowani ɗalibi da ya tsara lokacin karantunsa dai-dai da yawan kashe-kashen da ke kowane kwas, saboda a sami nasarar kamala su cikin lokaci. Idan ɗalibi ya kammala karatu cikin lokaci, yana da damar sake bitar abubuwan da aka yi a baya kafin jarabawar ƙarshen zangon karatu.

Muhimman abubuwan da suka shafi wannan kwas sun haɗa da:

a. Rarraba rukunin zuwa kashi – kashi (study units)
b. Manazarta da abubuwan kara nazari (reference)
c. Tambayoyi na auna fahimta (jinga). Assignment file
d. Tarin gabatar da Darasi (presentation schedule)

**Kashe-kashen Darasi (Study Units)**

Wannan manhajar ta kwas HAU105 tana ƙunshe da kashi-kashi har guda goma sha biyar. Ana bukatar a kammala kowane kashi cikin sati guda ne wanda ya haɗa har da amsa tambayoyi da ke ƙarshen kowane kashi da kuma amsa tambayoyin jinga idan akwai shi a ƙarshen darasin. Wannnan kashe-kashen su ne; -

**Rukuni Na 1 Ma'ana da Ire-Iren Adabi**

Kashi Na 1: Ma'anar Adabi
Kashi Na 2: Bambancin Adabi da Al'ada
Kashi Na 3: Asalin Faruwar Adabi
Kashi Na 4: Rabe-Raben Adabi
Kashi Na 5: Muhimmancin Adabi ga Rayuwar Al'umma

**Rukuni Na 2: Ma'anar Adabin Gargajiya**

Kashi Na 1: Ma'anar da Ire-Iren Adabin Gargajiya
Kashi Na 2: Zantukan Hikima
Kashi Na 3: Waƙar Baka

Kashi Na 4: Zube Na Baka
Kashi Na 5: Wasannin Kwaikwayo

**Rukuni Na 3: Adabin Zamani**
Kashi Na 1: Ma'anar Adabin Zamani
Kashi Na 2: Ire-Iren Adabin Zamani
Kashi Na 3: Rubutacciyar Waƙa
Kashi Na 4: Rubutaccen Zube
Kashi Na 5: Rubutaccen Wasan Kwaikwayo da Adabin Radiyo da Na Talbijin

**Manazarta da Abubuwan Ƙara Nazari**:
Akwai manazarta da aka kawo a ƙarshen kowane kashi waɗanda za su taimakawa ɗalibai ƙara nazari da zurfafa bincike. Wasu daga ciki litattafai ne waɗanda ba masu wuyar samu ba ne a ɗakunan sayar da littafai musamman waɗanda ke sayar da na Hausa. Akwai littafin adabi na Ɗangambo, (2008) da Gusau, (2011) waɗanda ya kamata a nemo su. Wasu kuma kundaye ne na kammala karatu digiri na ɗaya da na biyu hard a digirin digirgir, wasu kuma muƙalu ne ko dai a Mujallu ko waɗanda aka gabatar a tarurukan ƙara wa juna sani. Wasu daga ciki za a iya samunsa ta kafar sadarwa ta yanar gizo, ko kuma da taimakon ɗakunan karatu na Jami'o'i, musamman jamai'ar da take kula da "karatu daga gida" idan littattafan sun yi ƙaranci, ko kuma wuyar samu, to yana da kyau a yi amfani da bayanan da wannan manhajar kwas ɗin ya samar

**Auna Fahimta (Assignment).**
Ana jarraba ɗalibai domin gane fahimtar su a wannan kwas ta hanyoyi guda biyu ne. Hanya ta farko ita ce, ta ayyukan da ake ba ɗalibai su yi domin a gyara. Hanya ta biyu ita ce, wadda ake jarraba ɗalibai a ƙarshen zangon karatu (eɗamination). Da yake yanzu komi na koyarwa sun koma ta na'urar mai ƙwaƙwalwa ce, haka ma jingar da ake ba ɗalibai. Ana basu ne kuma suna amsawa da turowa nan take da zarar su gama amsa tambayoyin da aka yi masu. Daga ba tare da jimawa ba za su sami sakamakon jarrabawar da suka yi. Yana da kyau a kiyaye lokaci wajen amsa kowace tambaya domin yin haka kan taimaka wajen amsa tambayoyi duka cikin lokaci. Ana sa ran ɗalibai su amsa tambayoyin JINGA aƙalla guda uku waɗanda daga cikin ukun nan ne za a zavi ƙwarara guda biyu waɗanda ɗalibi ya fi samun maki don su kasance kashi talatin cikin ɗari na jararrawa (30%), sauran kashi saba'in (70%) ana samunsu ne a jarrabawar ƙarshen zangon karatu (semester eɗamination). Ita wannan jarrabawar zangon ƙarshen, ana yin ta ne ta hayar yanar gizo, saboda haka yana da kyau ɗalibai su kasance sun gwane da naƙaltar na'u'rorin kwamfuta saboda a sami cin jarrabawa yadda ya kamata.

**JINGA (Tutor Marked Assignment)**
Ana bukatar mai karatu ya ƙoƙarta gwada fahimtarsa ta hanyar amsa tambayoyin da ke ƙarshen kowane kashi. Ana sa ran ya san manufar kowane kashi na darussan da suka gabata. Saboda haka zai iya gwada fahimtarsa ta hanyar amsa tambayoyin da ke biye a kowane kashi. Duk da cewa jarrabawar da ake ba ɗalibai ta yanar gizo suke, duk da haka ɗalibai za su iya gwada fahimtarsu ta ƙoƙarin amsa tambayoyin da ke ƙarshen kowane kashi.

**Jarrabawa (Final Eɗamination and Grading)**
Kamar yadda aka ambata ne a baya, jarrabawa na ɗaukar kaso saba'in (70%) cikin ɗari na sakamakon da ya kamata ɗalibi ya samu. Akan ciro waɗannan tambayoyi daga cikin ire-iren waɗanda aka auna fahimtarsu ce a ƙarshen kowane kashi. Don haka yana da kyau ɗalibai su yi ƙoƙarin amsa tambayoyin da aka yi masu a ƙarshen kowane kashi da aka gabatar, yin amfani da kyakykyawar Hausa na ƙarawa amsar ɗalibi kwalliya.

**MAIN COURSE**

## CONTENTS


**Abubuwan Da Ke Ciki**

| | | |
|---|---|---|
| **Rukuni Na 1** | **Ma'ana da Ire-Iren Adabi** | |
| Kashi Na 1 | Ma'anar Adabi…………………….. | 1 |
| Kashi Na 2 | Bambancin Adabi da Al'ada………. | 5 |
| Kashi Na 3 | Asalin Faruwar Adabi……………… | 9 |
| Kashi Na 4 | Rabe-Raben Adabi………………… | 14 |
| Kashi Na 5 | Muhimmancin Adabi ga Rayuwar Al'umma…………………………… | 19 |
| **Rukuni Na 2** | **Ma'anar Adabin Gargajiya** | |
| Kashi Na 1 | Ma'anar da Ire-Iren Adabin Gargajiya | 23 |
| Kashi Na 2 | Zantukan Hikima…………………… | 29 |
| Kashi Na 3 | Waƙar Baka……………………….. | 34 |
| Kashi Na 4 | Zube Na Baka …………………….. | 40 |
| Kashi Na 5 | Wasannin Kwaikwayo……………… | 45 |
| **Rukuni Na 3** | **Adabin Zamani** | |
| Kashi Na 1 | Ma'anar Adabin Zamani…………… | 53 |
| Kashi Na 2 | Ire-Iren Adabin Zamani……………. | 58 |
| Kashi Na 3 | Rubutacciyar Waƙa………………… | 64 |
| Kashi Na 4 | Rubutaccen Zube…………………… | 72 |
| Kashi Na 5 | Rubutaccen Wasan Kwaikwayo da Adabin Radiyo da Na Talbijin……… | 80 |

**Ga fuskar yadda darasin zai kasance**

**Rukuni Na 1 Ma’ana da Ire-Iren Adabi**
Kashi Na 1 Ma’anar Adabi
Kashi Na 2 Bambancin Adabi da Al’ada
Kashi Na 3 Asalin Faruwar Adabi
Kashi Na 4 Rabe-Raben Adabi
Kashi Na 5 Muhimmancin Adabi ga Rayuwar Al’umma

## KASHI NA 1 MA’ANAR ADABI

**Abubuwan Da Ke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma’anar Adabi
  1.3.1 Ma’ana ta Zahiri
  1.3.2 Ma’ana ta Lugga
  1.3.3 Ma’ana ta Ilmi/Adabi
  Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Kalmar adabi ta tsiro ne daga wata kalmar aro **al`adab**, wadda take daga larabci, an aro kalmar daga larabci wadda take da ma`ana ta daban da wadda aka san ta da ita yanzu. Ko a larabcin, kalmar adab ta sauya ma`anoni da dama, a Hausa ma tana da ma`anarta da ta kevanta da nazari, a wannan darasi, za duba ma`anar wannan kalma da kuma abubuwan da ta ƙunsa a Hausa.



### 1.2 Manufofin Bincike

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Gane asalin kalmar adabi
- Gane manufarta a sauyi na farko da na biyu da ma`ana a mataki na uku.
- Ma`anar adabi ta waɗannan vangarori:

Ma`anar adabi ta zahiri
Ma`ana ta lugga
Ma`ana ta ilmi ko adabance.

## 1.3 Ma`anar Adabi

Adabi kalma ce ta aro wadda take da ma`anoni guda uku. An aro kalmar ce daga larabci aka yi mata kwaskwarima ta zama bahaushiyar kalma. Da farko akwai ma`anarta ta asali wadda ake wa laƙabi da ma`ana ta zahiri da ma`ana ta lugga, sa`annan ma`ana ta ilmi.

### 3.1.1 Ma`ana Ta Zahiri

Adabi, kamar yadda masana suka bayyana (Ɗangambo, 2008 da Gusau, 2011) kalma ce wadda asalinta daga larabci take. Kalmar adab wadda ita ce asalin kalmar adabi tana da ma`ana ta zahiri wadda ke nufin kiran liyafa. Idan Bahaushe ya ce ya adabance ka, to yana nufin ya gayyce ka kiran liyafa zuwa gidansa. Wannan na nuna cewa da farko ma`anar Kalmar kenan a Hausa 'Kiran Liyafa'. Abin da liyafa ke nufi anan shi ne gayyata zuwa ga cin abinci, ita kanta Kalmar liyafa kalma c eta larabci, don haka duk wanda ya ce ya adabce ka to yana nufin ya gayyace ka liyafa gidansa kenan, wannan ita ce ma`anar kalmar adabi ta zahiri.

### 3.1.2 Ma'ana Ta Lugga

Ma`anar abu ta lugga na iya kasancewa ma`ana ta harshe wato yadda harshe ya ƙirƙiri kalmar, ko kuma tana iya zama ma`ana ta asali wato ma`anar da kalma take da ita tun asali kafin ta sake da wata ma`anar. A Larabce, ta hanyar lugga kalmar adab na iya ɗaukar manufar "halaye na gari ko ɗabi'u masu kyau (wataƙila, a bisa hasashe, wannan ma'anar ita Hausawa suka fara ɗauka suka bai wa al-adab suka Hausance ta zuwa "Ladabi, wato nuna ɗa'a ko ƙasƙantar da kai, da biyayya, da sauran halaye na kirki da nagarta), Ɗangambo, (2008:4).

### 3.1.3 Ma'ana ta Ilmi/Adabi

Da Bahaushe ya ari kalmar adab, sai ya ƙara mata wasalin /i/ a ƙarshen gavar ta koma adabi mai sabuwar ma`ana a fanni nazari. Kalmar Adabi na nufin fasahar al'umma wadda ta jivanci harshe, ana wanzar da ita ne a magance ko a rubuce. Adabi na nufin hikima, da fasaha, da dabarar al'umma a cikin harshe, ya ƙunshi ƙirƙira da ka, a adana a ka ko a rubuce ko a wanzar da shi a aikace. Da wannan ne masana irin su Ɗangambo, (2008) da Gusau, (2011), sun bayyana ma`anar adabi kamar haka:

Ɗangambo, (2008:2) ya bayyana ma`anar adabi da cewa:

‘Zantuttukan da suka ƙunshi fasaha ko suke bayyana nau`o`in azanci a fannonin rayuwa iri daban-daban domin koya wani darasi ga al`umma, walau cikin furuci ko a rubuce’

Gusau, (2011:3) na cewa:
Adabin Hausa, adabi ne wanda ya shafi hikimomi da sarrafa harshe da kuma hanyoyi waɗanda suka shafi tafiyar da rayuwa ta yau da kullum, kuma yakan zama mai yin darasi da hannunka-mai-sanda ko mai barbaɗa gishiri a rayuwa.

Ƙamusun Hausa (2006:2) ya bayyana ma’anar adabi da “wani fanni na ilimi da ya ƙunshi labarai da waƙoƙin baka da rubutattu da wasannin kwaikwayo da al’adu da abubuwan fasaha da kimiyya”. Sannan Umar (1987:5) ya bayyana adabi da nufin sarrafa harshen Hausa mai ƙunshe da hikima ta musamman.

Idan aka nazarci ma`anonin da masana suka gabatar, za a fahinci cewa adabi ba wani abu ba ne illa hikima da fasahar al`umma waɗanda suka ƙunshi sarrafa harshe a cikin tsarin waƙoƙi ko ƙirƙirarrun labarai ko wasan kwaikwayo ko kuma wasu zantukan hikima na Hausa. Wasu na bayyana adabi da a matsayin madubi wadda ke bayyana hoton rayuwar al`umma. Wato idan ka ɗauki madubi, yadda za ka iya ganin siffarka a ciki haka za ka iya ganin hoton rayuwar al`ummar da ta shuɗe. Idan aka ɗauki wata waƙa ta baka ko rubutacciya, za a iya ganin yadda aka sarrafa harshe wajen ƙera wannan waƙar. Haka kuma za a ga hoton rayuwar wanda aka yi wa waƙar har da yadda shi mawaƙin ya ɗauki rayuwa. Idan ma a zube ne haka abin yake, bare fa a faɗa fannin wasan kwaikwayo.

Auna Fahimta

1- Mene ne ma’ana ta lugga?
2- Kalmar adab na iya ɗaukar manufar ____________

## 1.4 Taƙaitawa

Babu wani ƙayyadadden lokacin da za a ce kalmar ta sauya zuwa ga ma`anoni ko yanayin da ta koma, ma`anarta ta farko mai nufin kiran liyafada kuma ma`anarta ta lugga mai nufin halin ɗa`a ko da sauransu zuwa ma`anarta ta ilmi mai nufi hikimomi da fasahar al`umma wadda ta jibinci harshe, ana ƙirƙirar waɗannan fasahohi da ka a adana a ka, ko a wani abin rubutu ko kuma a a wanzar ta b aka ko a rubuce. Waɗannan su ne ma`anonin adabi da suka kamata kowane mai nazari ya sani.

## 1.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Adabi: - na nufin sarrafa harshen Hausa mai ƙunshe da hikima ta musamman.

## 1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

…………. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano, Bayero University.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*.Kano: Century Research and publishing Limited.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

Mene ne ma’ana ta lugga?
Ita ma`ana ta harshe wato yadda harshe ya ƙirƙiri kalmar, ko kuma tana iya zama ma`ana ta asali wato ma`anar da kalma take da ita tun asali kafin wata sabuwar ma`ana.

2-kalmar adab na iya ɗaukar manufar __________
- halaye na gari ko ɗabi’u masu kyau

## KASHI NA BIYU BAMBANCIN ADABI DA AL'ADA

### Abubuwan da ke ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma'anar Al'ada ta Zahiri
2.3.1 Ma'anar Al'ada ta Lugga.
2.3.2 Ma'anar Al'ada ta Ilimi
Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

Wannan darasi zan nuna wa mai karatu cewa akwai bambanci tsakanin waɗannan kalmomi guda biyu waɗanda suke tafiya kafaɗa-kafaɗa da juna. Adabi da al`ada tamkar Ɗanjuma da Ɗanjumai ne. Duk da yake suna yi wa juna shigar jiga-gizai, akwai wuraren da suka bambant. Waɗannann bambance-bambance su ake sa ran a gani a wannan darasi.

### 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Gane cewa ana iya samun abubuwa da yawa na adabi a fannonin al`alada.
- Bayanan al`adu a cikin ayyukan adabi.

### 2.3 Ma'anar Al'ada ta Zahiri

Ma`anar al`ada ta zahiri na nufin 'haila' wato jinin nan da mata yi wata wata. Allah ya hhallicci mace da fitar da wani jinni matuƙar bat a da juna biyu. Irin wannan jinni da mata ke fitarwa ya danganta da yanayin mace. Wata macen duk ƙarshen wata wannan jinni yak e zuwa mata, wata kuwa sai bayan watanni biyu biyu, wata ma har wata uku uku take yi kafin tag a jinni. Wata ba ta yi sai daga shekara sai shekara. Irin wannan jinni da ke fita a jikin mace a wannan lokaci shi ake nufi da

al`adar. Wato jinin al`adar da take fitarwa bayan wani ayyanannen lokaci.

### 2.3.1 Ma'anar Al'ada ta Lugga

Kalmar al`ada baƙuwar kalma ce wadda aka aro ta daga larabci, Baya ga ma`anarta ta zahiri, al`ada na nufin binwata hanya wadda aka saba da ita tun tale tale. Wannan na nufin bin wata hanya don yin maganin gargajiya, misali yin magani ta hanyar ganyeyyaki o tofi ko turare ko karatu ko hayaƙi ko surface. Duk waɗannan hanyoyi da aka lissafta su suns nuna hanya c eta al`ada wajen warkar da ciwo ko wata damuwa.
Abin lura a nan shi ne, a cikin al'adu na Hausawa, akan sami yanayi ko lokacin da waɗannan abubuwa ba sa samuwa sai da kalmomi na sarrafa harshe da gwanintar harshe. Misali, idan an ɗauki al'adar Hausawa da suka danganci.

- Ibada
- Zamantakewa (Aure, Biki, d.s)
- Neman abinci (Sana'o'i)

Za a tarar cewa kusan a duk cikin waɗannan nau'o'in al'adar za a sami zantuttukan ko waƙoƙin da suke danganci waɗannan bigire-bigiren da ake zance. Don haka ashe al`adar daban, adabi daban.

Haka kuma, inda su kansu waɗannan bigiren al'adun suke tamkar tsoka, haka nan zantuttukan hikima na harshe suke kamar jini da basa rabuwa. Wato duk wani aiki na adabi baya tafiya face sai a wani bigire na al`ada.

Wani vangaren da za a iya hasashen cewa akwai bambanci shi ne inda al'ada ta zama a aikace ake yinta watau ta yi amfani da gaɓɓan jiki don aiwatar da ita, Adabin na zama jagora ko hanyar da za a nuna wannan manufar da ake ƙoƙarin isar wa.

Misali, Al'adar Bahaushe ce yin dave, ko daka, da Gaɗa da dai sauransu. To wajen wanzar da wannan aiki ba shi kammala sai an haɗa da hikimomi ko fasahohi da suka jivanci wannan bigiren kamar waƙoƙi da kaɗe-kaɗe da raye-raye.

Wata hanyar da za a iya hasashen bambancin adabi da al`ada ita ce, cewa ana iya ganin abubuwa na al'adu waɗanda ake kwatantawa a cikin rayuwa. A kan kai lokacin da idan wani ya aikata wani abin da ya sava wa al'ada, wannan mutum yakan zamo abin nuni, ko dariya da nufin cewa ya aikata abin da ba haka ake son shi ba. Shi kuwa Adabi a iya cewa wasu abubuwan an ƙirƙire su ne, idan aka yi tunanin kwatanta su a rayuwa ta zahiri ana iya fuskantar matsaloli da dama, galibi ma wasu ba za su iya kasancewa a rayuwa ta zahiri ba. Misali, Kirari ko Take, Waƙa

da ake kwatanta ƙarfin mutum da dabba ko wata jaruntaka ko matsayin da ba za a iya yi ba a rayuwa ta zahiri.

### 2.3.2 Ma'anar Al'ada ta Ilimi

Ma`anar al`ada ta ilmi na nufin abubuwn da mutum ya saba yi a rayuwarsa ta duniya. Ma`ana, duk wani tsari ko yanayin gudanar da rayuwa waɗanda mutane suka tsara wa kansu kuma suka yadda da su a matsayin wasu abubuwa waɗanda za su kasance masu yi masu jagora kan harkokinsu na rayuwa ita ake nufi da al`ada. Al`ada a wannan fanni na nufin tsarin da ya shafi yanayin rayuwa gaba ɗayanta da harkokin da mutane ke yin a zamansu na duniya. A taƙaice ma iya cewa abubuwa ne waɗanda suka shafi tun daga kan aure zuwa haihuwa da kuma mutuwa, wato gaba ɗayan yadda mutane suka tsara wa kansu wajen gudanar da rayuwarsu.

Auna Fahimta

1. Me ake nufi da al'ada ta zahiri?
2. Me ka/kika fahimta da al'ada ta ilimi?

### 2.4 Taƙaitawa

A wannan darasi mun fahinci muhimman wuraren da adabi ya bambanta da al`ada, al`adar kowace al`umma na nuni da irin tsarin da wannan al`umma ta yi wa kanta don gudanar da rayuwar mutanenta. Wajen gudanarwa, akan sami wasu hikimomi da fahahar da mutane ke nunawa a lokacin da ake gudanar da wani abu na al`ada. Misali, bukukuwan Hausawa al`ada ce, to yayin bukukuwan ana samun waƙe–waƙe da kaɗe-kaɗe da raye-raye, su waɗannan waƙe-waƙen su ne ayyukan adabi, bukin shi kanshi al`ad ace. Tatsuniya al`ad ace amma waƙoƙin da ke cikin tatsuniya adabi ne.

### 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Al`ada: - na nufin binwata hanya wadda aka saba da ita tun tale tale
Ma`anar al`ada ta ilmi: - na nufin abubuwn da mutum ya saba yi a rayuwarsa ta duniya,

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Edward, B. T. (1967) “The Science of Culture” Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**1.** Me ake nufi da al’ada ta zahiri?

Ma`anar al`ada ta zahiri na nufin ‘haila’ wato jinin nan da mata yi wata wata.

**2.** Me ka/kika fahimta da al’ada ta ilimi?

Ma`anar al`ada ta ilmi na nufin abubuwn da mutum ya saba yi a rayuwarsa ta duniya

## KASHI NA UKU ASALIN FARUWAR ADABI

### Abubuwan Da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Asalin Faruwar Adabi
    3.3.1 Riwayar Samuwar Kiɗa
    3.3.2 Riwayar Samuwar Tatsuniya
    3.3.3 Samuwar Waƙoƙi
    3.3.4 Samuwar Zantukan Hikima
    Auna Fahimta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

Masana irin su Ɗangambo (2008:7) sun bayyana cewa babu wani sahihin tarihi a rubuce da ya tabbatar da yadda rassan adabi suka faru, musamman ma adabi baka, tatsuniyoyi da karin magana da kacici-kacici da waƙoƙi da take da kirari da roƙo da zambo da sauransu duk abubuwa ne waɗanda ba za a iya cewa ga lokacin da suka fara wanzuwa a cikin al`umma ba. Saboda haka wannan darasi zai lelleƙa hasashen da ake yi na samuwar wasu sassan adabi musamman kiɗa da waƙa da tatsuniya da zantukanm hikima.

### 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Gane cewa `yan Adam na farko a duniya suna yawo a doron ƙasa ba tare da wani killataccen wurin da za kira shi da gari ko ƙasa ko yanki ba.
- Gane wuraren zama mutane
- Hasashen samuwar kiɗa da waƙa da tatsuniya.

## 3.3 Asalin Faruwar Adabi

Babu wani takamaiman lokaci ko wani abu a rubuce wanda zai bayyana ga lokacin da aka samar da ayyukan adabin baka. Saboda haka duk abubuwan da aka bayyana an yi ne bisa hasashe, ba kuma sun shafi al`ummar Hausawa kaɗai ba ne a`a sun shafi tarihin samuwar adabin baka ne a duniya. Ba a yi bayanin rubutaccen adabi ba, saboda shi rubutaccen adabi ana da sanin lokacin da aka fara rubuta shi, kuma duk abubuwan da aka same su a rubuce, za a iya ƙirdaden lokacin da kuma al`ummar da suka samar da wannan abu.

### 3.1.1 Riwayar Samuwar Kiɗa

Ana hasashen farauta da yaƙe-yaƙe suna iya haddasa kiɗan tauri, wai lokacin da ɗan Adam ke rayuwa ta yawon farauta yakan kama dabbobi ya kuma ci 'ya'yan itace. To wai wata rana sai wani ya kama wata dabba, ya feɗe fatar, to da yake ba ya buƙatar fatar sai kawai ya jefar da ita. Faɗawar nan da za ta yi sai ta faɗa kan wani fafararren kututture wanda ruwan sama ya rarake tsakiyarsa. Da fatar ta bushe sai ta kame gam-gam kamar an rufa ganga. Wata rana sai wani ya zo wajen, da ya ga fatar ta kame sai ya yi ƙoƙarin ya cire ta. A ƙoƙarin yin haka sai ya dinga bugun fatar, sai kuwa ya ji tana yin wata ƙara ko sauti mai jan hankali mai daɗi. Ya kirawo 'yan'uwansa su ma suka bubbuga suka ji. Suka yi ta mamaki. Sai ya zame musu al'ada kullum idan sun fito za su wuce ta wurin, ko kuma duk lokacin da suka yi nishaɗi sai su je wurin su dinga bugawa suna samun nishadi. Wai wannan shi ne asalin yadda aka gano ƙera ganga da kuma yin kiɗa, Ɗangambo, (2008).

### 3.1.2 Riwayar Samuwar Tatsuniya

Dangane da tatsuniya kuwa, an ruwaito cewa a yayin da ɗan Adam ya gama hidimominsa na neman abinci da rana, yakan huta da daddare. A wannan lokacin ne al`ummar kowane yanki kan taru domin su ba juna labarin abubuwan da suka yi a wannan rana da kuma abin da suka ci karo da su, manya daga ciki na bayanin yanayin yadda za su inganta rayuwarsu, su kuwa yara suna wasanninsu, a wannan lokaci ne aka rinƙa ba yara labarai waɗanda za su taimaka masu da basirar gudanar da rayuwarsu.

Ɗangambo, (2008). Ya amabci cewa waɗannan dalilai suka sa aka ƙirƙiro wasannin motsa jiki da 'yan labarai ga waɗanda su ba za su iya yin wasannin ba, misali tsofaffi da mata, waɗanda koyaushe su suke tare da yara. Sannu a hankali har suka gano cewa ai za a iya yin amfani da irin waɗannan labaran wajen koya wa yara abubuwa iri daban-daban,

kamar irin yadda za su kare kansu idan wata dabba ta biyo su, ko hana su wasu ɗabi'u da al'ummarsu ba ta so da kuma sa su yin waɗanda take so, da kiwon lafiya da dai sauran halayyar zamantakewar al'umma. Wato tatsuniya kamar ta zama makaranta kc nan bayan raha da nishaɗi da take bayarwa.

### 3.1.3 Samuwar Waƙoƙi

Ta vangaren waƙoƙi kuwa, Ɗangambo, (2008) ya bayyana hasashen samuwarsu, ana jin su ma sun samu lokaci mai tsawo can baya, kuma ga alama yaƙe-yaƙe da farauta waɗanda a sakamakonsu ake zuga ko yabon wanda duk ya yi wata bajinta, sun taka muhimmiyar rawa wajen ƙirƙiro waƙoƙi, ko lafuzzan da suka yi kama da waƙa, misali roƙon baka da kirari da take da sauransu. Mu'amalar zaman sarakuna ko "jarumai" a garuruwa su ma lallai sun taimaka. Kirari da waƙoƙi da zuga jarumai don su fita da ƙarfi a lokacin faɗa da abokan gaba na daga cikin dalilan da aka bayar wajen samuwar waƙa. Hasashen na nuna cewa mutanen da suka iya kururuta jarumi da kambama shi don ya fuskanci abokan gaba su ne kuma suke jinjina wa jarumi a lokacin da aka gama yaƙi. Irin wannan kururutawar da kambamawar su suka haifar da waƙa saboda a nuna gwanintar harsh eta hanyar zaven kalmomi don girmamawa ko kambamawa.

### 3.1.4 Samuwar Zantukan Hikima

Zantukan hikima irin su karin magana da Habaici da zambo da ƙarangiya da sarrafa harshe na 'yan kama da 'yan gambara da 'yan ƙoroso da 'yan hoto da malam nabuta ko 'yan galura da sauransu, ga alama su sun faru daga baya ne bayan ɗan Adam ya sami bunƙasa ta fuskar zamantakewa. Wato sai bayan tsarin zamantakewa da shugabanci da tattalin arziƙin al`umma sun kafu sa`annan aka same su.

Auna Fahimta

1. Dangane da asalin kiɗa, fatar da aka jefar kan me ta faɗa?
2. Karin magana da habaici da zambo da ƙarangiya sun shafi _________



### 3.4 Taƙaitawa

Muhimman abubuwan da suka fito fili a nan sun nuna cewa akwai waɗansu sana`o`i ko kuma tsarin zamantakewa walau ta jaruntaka ko ta son nuna gwaninta su suka samar da wasu sassan adabin baka. Mun ga

vullar kiɗa daga yadda fatar naman dajin da aka feɗe ta samar, sa`annan mum ga samuwau waƙa sanadiyyar yaƙe-yaƙe, Tsarin zamantakewa ya haifar da samuwar tatsuniya da zantukan hikima. Waɗannan abubuwa kamar yadda aka ambata hasashe-hasashe ne kurum domin babu wasu hujjoji da za su tabbatar da haka. Wani hanzari ba gudu ba, ana batun samuwar waɗannan abubuwa a duniya ne ba wai a cikin al`ummar Hausawa kawai ba.

### 3.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- kiɗan tauri: nau’in kiɗa ne da ake yi wa ‘yan tauri



### 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Edward, B. T. (1967) “The Science of Culture” Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Dangane da asalin kiɗa, fatar da aka jefar kan me ta faɗa?
- wani fafararren kututture wanda ruwan sama ya rarake tsakiyarsa
2. Karin magana da habaici da zambo da ƙarangiya sun shafi _________
- Zantuttukan hikima

## KASHI NA HUƊU RABE-RABEN ADABI

### Abubuwan da ke ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Rabe-Raben Adabin Hausa
4.3.1 Ra'ayoyi Game da Rabe-Raben Adabi
4.3.2 Adabi Kafin Zuwan Musulunci
4.3.3 Adabi Bayan Zuwan Musulunci
4.3.4 Adabi Bayan Zuwan Turawa
Auna Fahimta
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 4.1 Gabatarwa

Masana sun rarraba adabi zuwa gida-gida, wasu masanan sun yi amfani da lokaci wajen rarraba adabi, wato akwai lokacin da Bahaushe yake rayuwa shi kaɗai tare da tsarin bautarsa na gargajiya ba tare da cuɗanya da wasu alumma ba, wannan lokacin adabinsa daban kuma shi ake wa laƙabi da kafin zuwan musulunci. Haka nan kuma akwai lokacin da musulunci ya shigo ƙasar Hausa tun ma kafin Bahaushe ya yi cuɗanya da larabawa, wannan lokacin ma adabinsa daban domin an sami tasirin musulunci a adabin. Sa`annan zango na uku na sauyawar adabi shi ne zuwan turawa ƙasar Hausa, shi ma wannan lokaci adabinsa daban. Wasu kuwa sun yi amfani da zamanin iya karatu da rubutu, ta wannan hanyar za a iya raba adabi zuwa giuda biyu, wato na gargajiya da kuma na zamani.



### 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- rukunan da aka raba adabi
- dalilan da ya sa aka yi wannan rabon.
- gane irin sauyin da adabi ya samu sakamako cuɗanya da baƙin abubuwa ko al`adu.

## 4.3 Rabe-Raben Adabin Hausa

Yana da kyau mai karatu ya fahimci cewa akwai masana da manazarta da yawa da suka gabatar da litattafai ko ƙasidu ko rubuce-rubuce waɗanda ke bayanin yadda za a iya raba adabin Hausa. Wasu sun yi amfani da lokaci, wasu kuma yanayin irin adabin suka ɗauka wajen karkasa shi kashi-kashi. Ga dai kaɗan daga cikin muhimman bayanan da masana suka gabatar ta yadda za a iya rarraba adabin Hausa.

### 4.3.1 Ra'ayoyi Game da Rabe-Raben Adabi

Akwai ra`ayoyi mabambanta waɗanda masana suka gabatar ta hanyar da za a iya rarraba adabin Hausa. Wasu na ganin za a iya rarraba adabi ta fuskar gargajiya da zamani, wasu kuwa sana ganin za aiya rarraba adabi ta la`akari da irin cuɗanyar da Bahaushe ya yi da wasu al`umma. Duk in an nazarci waɗannan rabe-raben, akwai muhimmmin abu guda da ya bayyana cewa akwai adabi na da can can da kuma sabon tsari wanda ya sami vurbushin ko tasirin wani abu.

### 4.3.2 Adabi Kafin Zuwan Musulunci

Hikomomi da fasahar al`ummar Hausawa waɗanda suka gada tun daga kaka da kakanni su ne adabin kafin zuwan musulunci. Wato ire-iren waɗannan zantutttukan da Bahaushe yake da su kafin ya yi cuɗannya da baƙin al`ummomi su ake kira da adabi kafin zuwan musulunci. Sanannen abu ne cewa musulunci ya shigo ƙasar Hausa tun kafin Bahaushe ya yi hulɗa da larabawa.

### 4.3.3 Adabi Bayan Zuwan Musulunci

Malumfashi na cewa, Larabawa sun shigo ƙasar Hausa ta hanyoyi mabambanta, da farko dai a lokacin shigo da addinin Musulunci wanda aka ce ya samu karɓuwa tun wajajen ƙarni na 8 zuwa na 9, daga baya kuma ta hannun masu cinikin bayi da saye da sayarwa addinin Musulunci ya zaunu sosai a ƙasar Hausa. Daga tskanin ƙarni na 13 zuwa na 15 kuwa addinin Musulunci ya warwatsu zuwa garuruwa da ƙauyukan ƙasar Hausa, ta yadda kusan kowane sashe na ƙasar Hausa ana gudanar da addinin Musulunci. Wannan ya sanya ilmin addinin Musulunci da makarantun allo suka wanzu a kusan ko'ina a faɗn ƙasar Hausa. Wannan ne ya sa al'ummar yankin suka naƙalci harshen Larabci ta yadda har suka iya rubutu da shi, suka samar da hanyar rubutu ta ajami. Saboda haka har zuwa lokacin da aka jaddada addinin Musulunci a ƙasar Hausa a ƙarni na 19, za a ga cewa yawancin Hausawa sun iya karatu da rubutu cikin Larabci da ajami ta yadda aka samar da

rubutaccen adabin Hausawa ta waannan hanyoyin rubutu. Yawancin ayyukan adabin da aka samar sun fi a fagen waƙa da kuma zube. Ke nan wannan ya nuna mana cewa adabin da suak samu bayan zuwan addinin musulunci da iya rubutu da Ajami shi ake wa laƙabi da adabi bayan zuwan musulunci

### 4.3.4 Adabi Bayan Zuwan Turawa

Turawa da suka zo ƙasar Hausa sun sami mutane da ilmi na musulunci da kyakkyawar tsarin shugabanci da hanyoyi tarbiyar al`umma. Baya ga wannan sun iske mutane da adabinsu na gargajiya waɗanda wasunsu ba a rubuce suke. Abin nufi anan shi ne, Hauswa sun koyi karatu da rubutu cikin larabci hart a kaima sun iya fitar da haruffan Ajami wanda yake tsarin rubutu ne na musamman kuma an yi amfani das hi wajen rubuta waƙoƙi da zube. Da turawa suka iso sun iske Hausawa da tarin hikimomi da fasahar gargajiya wannan dalii ya sa sun yi yunƙurin mayar da waɗannan adabin baka zuwa rubutattun adabi ta hanyar amfani da haruffan book. Wannan shi ake nufi da rubutaccen adabi, wato said a turawa suka zo aka koyi karatu da rubutun book kana aka samar da ire-iren waɗannan adabin.

## 4.4 Adabin Gargajiya

Adabin gargajiya adabi ne da masana suka bayyana cewa, shi ne adabin da Hausawa ke da shi tun tale-tale, wato sun gaje shi ne tun daga kaka da kakanni, kuma yana da matuƙar muhimmanci ga rayuwar Hausawa ta fuskoki daban-daban. Wannan adabin ne wasu ke yi laƙabi da adabin ‘Ka’ ko adabin ‘Baka’, adabi gargajiya ba yana taƙaita ga lokacin da ya shuɗe ba ne, illa cewa ko a wannan zamani da muke ciki za a iya samu adabin gargajiya idan aka aiwatar da shi a bisa tsarin da aka gaje shi tun daga kaka da kakanni.

## 4.5 Adabin Zamani

Ɗangambo, (2008). Ya ce Adabin zamani shi ma, kamar yadda sunansa ya nuna, adabi ne wanda zamani ya kawo. Wato da can, kafin zuwan Musulunci da zuwan Turawa, babu shi. Shi wannan adabi, akan yi masa laƙabi da “rubutaccen adabi.” Kamar yadda muka gani a baya, adabin gargajiya, shi ba rubutacce ba ne asalinsa. Adabin zamani ya rabu gida uku:

Rubutattun waƙoƙi
Rubutun zube/ƙagaggun labarai
Wasan kwaikwayo (rubutacce)

Auna Fahimta

1. Wasu na ganin za a iya rarraba adabi ta fuskar ________
2. Hikomomi da fasahar al`ummar Hausawa waɗanda suka gada tun daga kaka da kakanni su ne adabin __________

## 4.5 Taƙaitawa

Bayanai sun gabata cewa za a iya raba adabi ta fuska biyu: Da farko idan an yi la`akari da yanayin zamantakewar Hausawa da irin tasirin da suka samu ta sanadiyyar cuɗanyansu da baƙin al`adu, za a iya raba adabi zuwa gida uku kamar haka: Adabi kafin zuwan musulunci, da adabi bayan zuwan musulunci da kuma adabi bayan zuwan turawa. Ta ɗaya vangaren kuwa, in an yi amfani da yanayin iya karatu da rubutu da kuma hanyar adana adabi, za a iya rarraba adabi gida biyu: Wato adabin gargajiya da adabin zamani.

## 5.6 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- ajami: tsarin rubutun Hausa ne da ake yi da harufan Larabci.
- Rayuwa: ci gaba da wanzuwa ko haɓaka ko ƙara girma

## 4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Wasu na ganin za a iya rarraba adabi ta fuskar _______
- gargajiya da zamani
2. Hikomomi da fasahar al`ummar Hausawa waɗanda suka gada tun daga kaka da kakanni su ne adabin _______________
- kafin zuwan musulunci.

# KASHI NA BIYAR MUHIMMANCIN ADABI GA RAYUWAR AL'UMMA

## Abubuwan da ke ciki

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufar Darasi
5.3 Muhimmancin Adabi
5.3.1 Ilmantarwa
5.3.2 Nishaɗantarwa
5.3.3 Adana Tarihi
5.3.4 Haskaka Rayuwa
5.3.5 Bunƙasa Harshe
5.3.6 Adana Al'adu
Auna Fahimta
5.4 Taƙaitawa
5.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 5.1 Gabatarwa

Adabi ko shakka babau yana da muhimmanci ga rayuwar alumma, kowace al`umma ta duniya tana taƙama da hikimomi da fasahar da suka gada kaka da akkanni, ire-iren waɗannan hikimomi da fasaha suna nuna ci gaban al`ummoma da irin falsafar su game da rayuwa. Ta hanyar adabin kowace al`umma za a iya gane lokacin da aka wanzar da wannan adabi da irin tasirin da wannan adabi ya yi ga mutane. Adabi na nuna irin nahiyar da mutanen suke, akwai lokutan da za a iya samun tarayya a tunani ko yanayin zartar da wasu abubuwan na adabi, irin wannan yanayi na nuni da tasirin da wani adabi ya yi ga wani sanadiyyar cuɗanya ko maƙwbtaka.



## 5.2 Manuofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Gane muhimmancin adabi ta kowace fuska.
- ilmantarwa da nishaɗantarwa
- kaifafa tunani da adana tarihi da taimakawa harshe wajen ƙirƙirar zantuttukan hikima waɗanda za su zama fitulu masu haskaka rayuwar al`umma.

## 5.3 Muhimmancin Adabi

### 5.3.1 Ilmantarwa

Akan yi amfani da Adabi wajen ilmantar da alumma akan abin da ba su sani ba, sau da yawa ayyukan adabi suna ilmantar da alumma kan wasu abubuwan da za su zama alfanu gare su. Fasihai masu rubuta zube ko wasan kwaikwayo ko waƙa suna lura da halin da al’umma suke ciki ne a lokacin da suke ayyukansu na adabi. Saboda haka, idan akwai wani baƙon abu day a bayyana a cikin alumma, ta wannan haya ana ya ilmantar da mutane ko kuma wayar masu da kai kan muhimmanciun wannan abu. Haka kuma ayyukan adabi suna zama abubuwan yanke hukunci ko gyara a cikin al'umma. Abun nufi a nan, idan an sami wani azzalumin mai sarauta ta hanyar amfani da Adabi ana iya nuna masa kurakuransa da abin da ya kamata ya yi.

### 5.3.2 Nishaɗantarwa

Adabi ko wasu nau'o'in Adabi sun kasance abokan hira ga al'umma da nishaɗai a lokacin da jiki yake buƙatar hutu. Bar ta batun hutu ma, har akan yi amfani da wasu nau'o'in Adabin domin ƙarin kuzari.

### 5.3.3 Adana Tarihi

A kan yi amfani da Adabi don adana tarihi. Idan an ɗauki wasu sassa na adabi, za a iya fahimtar yadda aka sarrafa harshe da irin tsarin ko ci gaban da harshe ya samu daga nan a fahimci irin rayuwar al'ummar da ake magana a kan su ta yin amfani da wannan nau'in Adabin.

### 5.3.4 Haskaka Rayuwa

Wannan na nuni da inda aka fito da inda ake har da ƙoƙarin haskaka gaba. Da yawa akwai waƙoƙin da suke nuni ko hannunka-mai-sanda ga al'ummar Hausawa kan wasu halaye marasa kyau day a kamata a kula da su domin a sami gyara a cikin alumma. Ba waƙa kaɗai ba, hatta sauran fannonin adabi wato zube ko was an kwaikwayo suna zama fitulu masu haskaka inda al`umma ta dosa. Wasu kuwa kira suke kan kyawawn halaye da ɗabi`u na gari waɗanda ya kamat muytane su siffantu da su. Haƙuri da jaruntaka da karimci da riƙon gaskiya da tausayi da cika al`ƙawari da amana na daga cikin ɗinbin halaye da ɗabiu waɗanda adabin Hausa yake kira ga alumma domin su rungume su.

### 5.3.5 Bunƙasa Harshe

Ƙyale-ƙyalen jawo hankali da gwaninta harshe da sarrafa kalmomi a cikin waƙa ko zube ko wasan kwaikwayo ko shakka babu suna taimakawa harshe ne. Sanannen abu ne cewa mai aikin adabi yana da lasisi na karya ƙaidar harshe domin waƙarsa ta tafi kamar yadda yake so, wannan ba yana nufin gazawa ce a harshe ba ko kuma a ce sun naƙasa harshen, illa ma wata fasaha ce wadda take samar da wasu kalmomi ko rumbuin kalmomi waɗanda za su zama abubuwan bincike ga masu nazartar harshe.

### 5.3.6 Adana Al'adu

Adabi da al`ada tamkar tsoka da jinni ne, saboda haka adabi na taimakawa wajen adana al`adun Hausawa. Adabi na taimakawa wajen adana al`adu domin ta hanyar adabi za a iya gane tsarin zamantakewar al`umma da yadda suke gudanar da rayuwarsu. Idan muka ɗaukimisalin tatsuniyar Ruwan Bagaja, a wannan tatsuniya akwaikyanayin zamantakewar Bahaushe wanda ke nuna cewar yana auren mata fiye da ɗaya, haka nan kuma yana nuna mana yadda aka fi fifita wata matar akan wata. Tatsuniyar na nuni da yadda abincin Hauswa suke in an duba kogunan kala-kalan abincin da aka ambata a cikin tatsuniyar. Akwaikma nuna tsarin shugabanci da yadda masarautu suke da abubuwan da mutane suka fi fiftwa a rayuwarsu da kuma abuuwan da suke ƙyƙma kamar yadda muka gani a sakamakon da `ya bora ta samu da na `yar mowa.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Adabi da al`ada tamkar _________ ne |
| 2- | Sanannen abu ne cewa mai aikin adabi yana da lasisi na ________domin waƙarsa ta tafi kamar yadda yake so. |

### 5.4 Taƙaitawa

Abubuwan da suka fito fili a wannan darasin sun nuna cewa adabi da nazarinsa suna da muhimmanci ta waɗannan hanyoyi: Da farko dai adabi, na ilmantarwa da faɗakarwa da nishaddɗantarwa. Adabi na kyautata dangantaka da haɗin kan al`umma da tarbiyya da koyarwa. Haƙiƙa adabin baka ko na gargajiya ya kasance tankar makaranta ce ta koyar da al`umma yanayin zaman rayuwa.

## 5.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- alfanu: amfani

## 5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Adabi da al`ada tamkar ne
- tsoka da jinni
2. Sanannen abu ne cewa mai aikin adabi yana da lasisi na domin waƙarsa ta tafi kamar yadda yake so.
- karya ƙaidar harshe

## RUKUNI NA 2 MA’ANAR ADABIN GARGAJIYA

Kashi Na 1 Ma’anar da Ire-Iren Adabin Gargajiya
Kashi Na 2 Zantukan Hikima
Kashi Na 3 Waƙar Baka
Kashi Na 4 Zube Na Baka
Kashi Na 5 Wasannin Kwaikwayo

## KASHI NA 1 MA’ANAR DA IRE-IREN ADABIN GARGAJIYA

**Abubuwan da suke ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma’anar Gargajiya
  1.3.1 Ma’anar Adabin Baka
  1.3.2 Ma’anar Adabin Ka
1.4 Ire-Iren Adabin Gargajiya
  1.4.1 Zantukan Hikima
  1.4.2 Waƙar Baka
  1.4.3 Zube Na Baka
  1.4.4 Wasanni
  Auna Fahimta
1.5 Taƙaitawa
1.6 Ma’anar Muhimman Kalmomi
1.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan adabin gargajiya, wato adabin da ya wanzu tun kafin Bahaushe ya sami hanyar rubutu da karatu sakamakon haɗuwa da baƙin al’ummu. A wannan gavar za a daddale bayanin adabin **baka** da adabin **ka** don fayyace Rukuninsu a adabin gargajiya. Haka nan kuma kashin ya ƙunshi bayanai kan ire-iren adabin gargajiya, wato adabin da ake ƙagawa a ka, a wanzar da baki, a adana a ka. A wannan gavar za a kawo bayanin ire-iren adabin gargajiya waɗanda suka haɗa da zantukan hikima da waƙar baka da zube na baka da wasanni.

## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma'anar adabin gargajiya
- Ma'anar adabin baka
- Ma'anar adabin ka,
- Ire-iren adabin gargajiya
- Mene ne zube na baka ?
- Yaya wasannin gargajiya suke ?

## 1.3 Ma'anar Gargajiya

Kalmar gargajiya daga 'gado' ne, wato duk abin da aka ce na gargajiya ne ana danganta shi da abin da aka gada kaka da kakanni, tun kafin Hausawa su haɗu da wata al'umma har ta yi naso a cikinta. Duk wani abu na gargajiya bas hi da nasaba da rubutu, ko da kuwa an rubuta shi daga baya domin adanawa bai sauya masa suna daga na gargajiya ba sai dai a iya cewa an zamanantar da gargajiyar.

### 1.3.1 Ma'anar Adabin Baka

Idan aka ce adabin baka, ana nufi adabin gargajiya ne wanda ba rubutacce ba ne, kuma adabi ne da yake ƙunshe cikin cikin rayuwar yau da kullum wanda tushensa daga iyaye da kakanni ne. (Ɗangambo, 2008). Kiran sa adabin baka yana da nasaba da wanzar da shi da fatar baki da ake yi.

### 1.3.2 Ma'anar Adabin Ka

Adabin Ka da Adabin Baka duk abu guda ne, adabi ne da ake ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka. Rawar da kai ke takawa wajen ƙagawa da adanawa ya sanya wasu masanan ke bayyana shi da adabin ka maimakon adabin gargajiya ko adabin baka. Saboda haka, abin da ke da muhimmanci a nan ba sunan ba, amma da zarar an ce adabin ka ko adabin baka ko adabin gargajiya, ana nufin adabin da ake ƙirƙirar sa a ka, a wanzar da fatar baki, a kuma adana a ƙwaƙwalwa ba tare da rubutu ba ko wata na'ura ta zamani.

## 1.4 Ire-Iren Adabin Gargajiya

Adabin gargajiya ya kasu gida uku ko huɗu a wani haujin, akwai waƙar baka da zube na baka da wasanni da zantukan hikima.

### 1.4.1 Zantukan Hikima

Zantukan hikima na nufin guntattakin zantuka masu cike da hikima, a wani lokacin ƙunshe da faffaɗar ma'ana. Galibi ba su cika tsayi ba a furuci, sai dai idan aka yi sharhinsu ta fuskar hoton da suke haskawa a rayuwar al'umma sai a tarar suna da faɗin gaske. Misalan waɗannan zantukan hikima sun haɗa da karin magana da take da kirari da habaici da zambo da salon magana da zaurance da sauransu.

### 1.4.2 Waƙar Baka

Akwai wasu matakai wato kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma'anar waƙar baka, waɗannan kalmomi sun haɗa da rerawa da hawa da saukar murya da daidaita murya da rauji da naƙaltar harshe da hikima da fasaha da kiɗa da karvi ko amshi (Gusau, 2008).

Gusau (1984), ya bayyana waƙar baka da cewa, "wani saƙo ne cikin zance da azanci da ake rerawa ba faɗa kurum ba, ta hikima da fasaha da zavavvun kalmomi waɗanda suka dace da saƙon, kuma tana zuwa gunduwa-gunduwa da sautin murya da kiɗa da armashi da gaɗa da tafi mai saka zuciya jin daɗi."

Saboda haka, waƙoƙin baka kamar yadda sunansu ya nuna, su ne waƙoƙin da aka yi da baki. Abin nufi a nan shi ne, su dai waƙoƙin baka shirya su ake yi a zuci, kuma a gabatar wa mutane da su ta hanyar rera su da baki. Tun ainihinsu ba a rubuce suke ba, kuma mawaƙan da suke tsara su, ba a rubuce suke tsara su ba, sun vullo da su ne ta hanyar rerawa da baki, wani lokaci tare da kiɗa, wani lokaci kuma babu, (Tsoho (1983:1). Waƙoƙin baka sun ƙunshi waƙoƙin mata na aikace-aikacen cikin gida da waƙoƙin yara na dandali da waƙoƙin cikin tatsuniyoyi da kuma waƙoƙin makaɗa da mawaƙan Hausa na gargajiya.

### 1.4.3 Zube Na Baka

Ana iya bayyana zube na baka da wata hikima, ko basira ko tunani irin na ɗan'Adam da ya ƙaga kan wani abu, ya furta da fatar baki domin watsa wata manufa don koyarwa ko kuma hannunka-mai-sanda da jagora don nishaɗi.

Saboda haka, zube na baka ya ƙunshi waɗansu labarai masu ɗan tsawo, ana kuma yin su ne a lokacin hira kamar, labarai na jarumai ko `yan fashi ko na almara, irin su labaran hikima ko wasa ƙwaƙwalwa da kuma tatsuniyoyi irin na gizo da ƙoƙi da hikayoyi da ƙissa da tarihi ko tarihihi da tatsuniya da zaurance da salon magana da kirari da take da zambo da sauransu da dama. Duk irin waɗannan nau'o'i na zube da aka ambata

ana ƙaga su ne a ka, a wanzar da su da baka, a kuma adana a ka. Shi ya sa ake kiran su zube na baka.

### 1.4.4 Wasanni

Wasanni jam’i ne na kalmar wasa wadda kalma ce da ake amfani da ita domin bayyana wani abu da yake sanya nishaɗi ko jin daɗi da raha da walwala a zukatan masu yi ko masu sauraro. Gusau, (2013), cewa ya yi wasan yara yana nufin wasu hanyoyi da dabaru waɗanda yara maza da mata suke amfani da su na tsinka jininsu da motsa jiki tare da cinye lokaci da samun walwala da naƙaltar dabarun zaman rayuwa cikin nishaɗi. A gargajiyance, ba yara ne kawai ke wasanni ba, akwai wasannin gargajiya waɗanda sukan ƙunshi motsa jiki da motsa tunani don bayyana gwanintar Bahaushe. Saboda haka za mu iya karkasa wasannin zuwa gida-gida kamar haka:

- Wasannin gargajiya na wasa kurum: Wasan kura ko na maciji ko na kunama.
- Wasannin sana'a da suka haɗa da wasan gardawa (hawan ƙaho) da na ‘yan tauri (wasan tauri) da na ‘yan kama da na ‘yan dabo.
- Wasannin dandali ko wasannin yara da suka haɗa da A sha ruwan tsuntsaye da ɗan akuyana da na ‘Yar tsana.

Wasannin bukukuwan al'ada da suka ƙunshi wasan Giwa sha laka da Bikin buɗin daji da na Kallankuwa da wasan bori.

Auna Fahimta

1. Kawo ire-iren adabin gargajiya
2. Me ake nufi da kalmar waƙar baka

## 1.5 Taƙaitawa

Wannan kashi ya ƙunshi bayani ne kan adabin gargajiya. An bayyana ma’anar gargajiya, sai aka bayyana ma’anar adabin baka da kuma nuna yadda adabin ka yake ta fuskar ƙirƙira da wanzarwa da adanawa, sai aka fahimci cewa duk abu guda ne. Haka nan a wannan kashi, an tattauna ire-iren adabin gargajiya waɗanda suka haɗa da zantukan hikima da waƙar baka da zube na baka da kuma wasanni.

## 1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Wasa: kalma ce da ake amfani da ita domin bayyana wani abu da yake sanya nishaɗi ko jin daɗi da raha da walwala a zukatan masu yi ko masu sauraro.



## 1.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Kawo ire-iren adabin gargajiya

- Zantukan hikima
- Waƙar Baka
- Zube Na Baka
- Wasanni

2. Me ake nufi da kalmar waƙar baka

Waƙar baka da cewa; “wani saƙo ne cikin zance da azanci da ake rerawa ba faɗa kurum ba, ta hikima da fasaha da zavavvun kalmomi waɗanda suka dace da saƙon, kuma tana zuwa gunduwa-gunduwa da sautin murya da kiɗa da armashi da gaɗa da tafi mai saka zuciya jin daɗi.”

# KASHI NA BIYU ZANTUKAN HIKIMA

## Abubuwan da suke ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Zantukan hikima
 2.3.2 Hausawa A Zamanin Annabi Adamu
 2.3.3 Harshen Hausa A Zamanin Annabi Adamu
 Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

Daga cikin dabaraun da Bahaushe ke amfani wajen koyar da darussan rayuwa da kaifafa tunani da cusa kyawawan ɗabi’u cikin al’umma akwai maganganunsa na azanci ko zantukan hikima da sauransu. Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan zantukan hikima da ire-irensa kamar karin magana da take da kirari da habaici da zambo da salon magana.

## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Guntattakin zantukan hikima na Hausa da ire-irensu.
- Ma’anar zantukan hikima
- Ire-iren zantukan hikima na Hausa
- Fayyace nau’o’i da misalan zantukan hikima
- Bayyana matsayin zantukan hikima a adabin Hausa

## 2.3 Zantukan Hikima

Zantukan hikima su ma nau’i ne na adabi, wato fasahar al’umma wadda ta jivanci guntattakin zantuka masu cike da hikima, a wani lokacin ƙunshe da faffaɗar ma’ana. Galibi ba su cika tsayi ba a furuci, sai dai idan aka yi sharhinsu ta fuskar hoton da suke haskawa a rayuwar al’umma sai a tarar suna da faɗin gaske.

### 2.3.1 Ire-Iren Zantukan Hikima

Ire-iren zantukan hikima sun haɗa da karin magana da take da kirari da habaici da zambo da salon magana da sauransu.

### 2.3.2 Karin Magana

Karin magana zance ne a dunƙule mai faffaɗar ma'ana, wato wata gajeriyar magana ce ƙunshe da voyayyiyar ma'ana ko dogon bayani in aka warware. Shi ya sa karin magana take da siffofin da suka keventa gare ta, wato gajarta da gavovi biyu da dunƙulewa da kuma reɗe ko fid da wasu kalmomi da ba dole sai an yi amfani da su ba.

Da yake kalmomi biyu ne suka gina karin magana, wato '*kari*' da kuma '*magana*'. Kari na nufin wani vangare ko rabi ko karyayye ko kuma rababbe. Magana kuma na nufin zance ko furuci ko kalami da mutum kan yi domin a fahimci abin da ke cikin zuciyarsa. Ke nan karin magana zance ne da aka yi wa givi ko aka karya shi ko raba shi ko kuma aka kawo wani vangare aka yi watsi da wani vangaren (Malumfashi, 2018).

Yawancin karin maganar Hausa vangare biyu gare su, vanagare na biyu shi ke ciko bayanin vangare na farkon. Misali:

i. "Allah na mutane", java ta ga bakin mijinta
ii. "Da haka muka fara", kuturu ya ga mai ƙyasfi.
iii. "Da sauran tsalle", in ji varawon dankali.
iv. "Abin da daɗi", an ba mayya tsaron gawa.
v. "Yaushe kuma?", an ce da kuturu ka gama lafiya. Da sauransu.

### 2.3.3 Take da Kirari

Take ya samu ne daga kalmar *takawa,* wato a yaba ka ko kwarzanta ko zuga kai, da zai sa ka jirga ko ka taka saboda ka ji daɗin abin nan da ka ji ko saurara. Akan yi take da kiɗa ko wasu furuci da suke danganta abin da ake kaɗa wa taken da shi. Saboda haka take wani amo ko zance da ke share fage kafin kirari ya iso. Ana yin take ne da kiɗa ko busa ko wani salo da za a iya fassarawa a magananance. Misali, kafin fara farauta akan yi kiɗa don sanar da jama'a cewa za a fita, kuma wannan kiɗan yakan zo a matsayin taken wani ɗan farauta ne. Sa'annan take kan iya zama wani vangare na ƙoƙarin yabo ko kushewa ga abubuwan da jama'a suka sa gaba, sai dai take bai cika tsawo ba. Sai dai duk da yake take yana zuwa da amo ne, ba zance ko furuci ne ba, da zarar aka yi wa mutum take zai iya vugewa da yin kirari.

Kirari furuci ne wanda ya yi kama da yabo, ta amfani da kalmomin ciccivawa da ake yi wa wani mutum cikin hikima don a kambama shi ko wani abu don a fito da kyawonsa da armashinsa a idon jama'a. A tsarin

kirari, za a kira mutum ne ta hanyar amfani da sunansa ko ta ambaton siffofinsa waɗanda abin tutiya ne ko a wajen mai yin kirarin. Har ila yau, kirari kan iya ƙunsar kalaman da in ba a muhalli na kirarin ba, bas a ambatuwa kai-tsaye ga mutum. Misali kalmomi irin su 'shege' ko 'mahaukaci' ko 'arne' da sauransu. Mutum na iya yi wa kansa kirari, ko ya yi wa wani ko wani ya yi masa. Alal misali:

i. Sai ni baƙi fentin Allah, mahaukacin kare mijin Ladidi
ii. Damo sarkin haƙuri ƙanin su Talatu
iii. Hajiya Balaraba ɗiyar Tijjani,
iv. Tabbara uwar alƙawari,
 Sukari ba ki farin banza ba,
v. Masara mai yawan zane ta Alhaji Audu.
vi. Kunu ɗan babban masaki,

Shanka banza barin ka banza,
Da safe marmari da maraice ciwo,
Ya vata ruwa ya vata wuta ya je ciki bai yi komai ba,
A kira ka da tsinin baki a sha ka da tsinin baki.

Daga misalan da suka gabata, mun fahimci ana gina kirari da siffa ko halayyar mutum ko abin da za a kirara, akan kuma danganta abu da makusantarsa misali miji da mata ko 'yan'uwa da sauransu. Sa'annan, ana iya yi wa mutum ko dabba ko gari ko abinci ko itaciya ko wani abu mai rai ko mara rai kirari.

### 2.3.4 Habaici da Zambo

Habaici riga ce ba wuya duk wanda ya sa ta yi masa daidai, wato dai tamkar yi da mutum ne ta magana a voye, ma`ana zagi mai mayafi. Wato ba a fito fili aka zagi mutum ba amma akan faɗi wasu kammanu ko kuma hali nasa yadda daga ji za a fahimci ko da wa ake. A habaici akwai `yar gaskiya game da halaye ko 'yar ya, sai dai ƙarya ta fi yawa. A tsarin habaici ba a siffanta wanda ake yi wa shi, sai dai a yi domin ya gane ko wasu su fahimta cewa an san abin da shi yake yi.

Zambo kuwa a ɗaya vangaren yana nufin kishiyar yabo. Inda akan siffanta mutum da wasu siffofi munana waɗanda za su wulaƙanta shi ko su jawo masa rashin martaba a idon mutane, ba tare da la'akari ko wannan mutum yana da waɗannan siffofi ko ba shi da su ba. Akan ƙara gishiri a zambo don a daɗa lalata hali ko ɗabi'ar wanda ake yi wa shi, (Gusau, 2008:380).

A dunƙule, habaici suka ce a kaikaice, tamkar dai riga ba wuya, duk wanda ya sa ta yi daidai da shi, zambo kuwa suka ce kai-tsaye har ma akan ƙara gishiri ko a wuce-makaɗi-da-rawa.

### 2.3.5 Salon Magana

Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari zance ne mai ɗauke ko ƙunshe da wasu kalmomi masu wuya ko masu kama da juna, yakan ƙunshi luguden kalmomi. Misali ;

i. Tun da Tavo take ba ta tava tava tavo ba
ii. Tattabara tara ƙwai tara ɗa tara za ta gari tara gai da mutum tara
iii. Ke matar Dubarudu ba ni madubin Dubarudu in duba. Ni ma matar Dubarudu ban duba madubin Dubarudu ba, sai kai baƙon Dubarudu ka ce in ba ka madubin Dubarudu ka duba ?
iv. Na je Duru na iske durumin Duru na ce durumin Duru me ya sa mutanen Duru suke sarar ka da duru-duru ? da sauransu da dama.

Auna Fahimta

| |
|---|
| 1. Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari zance ne mai ɗauke da wasu ______ kalmomi masu wuya ko masu kama da juna.<br>2. Habaici ___________duk wanda ya sa ta yi masa daidai riga ce ba wuya |

### 2.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an tattauna a kan zantukan hikima, wato maganganu na azanci waɗanda Bahaushe ke amfani wajen koyar da darussan rayuwa da kaifafa tunani da cusa kyawawan ɗabi'u cikin al'umma. Kashin ya ƙunshi bayanai kan zantukan hikima da ire-irensa kamar karin magana da take da kirari da habaici da zambo da salon magana.

### 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Take : - kalma ce mai nufin yaba kai ko kwarzanta ko zuga kai.
- Karin Magana: - zance ne a dunƙule mai faffaɗar ma'ana, wato wata gajeriyar magana ce ƙunshe da voyayyiyar ma'ana ko dogon bayani in aka warware.

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa*. Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa*. Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari zance ne mai ɗauke da wasu _____ - kalmomi masu wuya ko masu kama da juna.
2. Habaici duk wanda ya sa ta yi masa daidai.

- riga ce ba wuya

# KASHI NA UKU WAƘAR BAKA

## Abubuwan da suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Waƙar baka
3.3.1 Ma'anar Makaɗa
3.3.2 Rabe-Raben Makaɗa
3.3.3 Siffofin Waƙar Baka
3.3.4 Kayan Kiɗa
Auna Fahimta na 1
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 3.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya ƙunshi bayani ne kan waƙar baka da ƙunshiyarta. A ciki an yi ƙoƙarin kawo ma'ana da kuma siffofin waƙar baka. Haka kuma za a kawo ma'ana da rabe-raben makaɗa. Daga bisani kuma za a kawo bayani kan kayan kiɗa.



## 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma'anar waƙar baka da siffofinta
- Rabe-raben makaɗa
- Kayan kidan da ake amfani da su.



## 3.3 Ma'anar Waƙar Baka

Masana da dama sun bayyana ma'anar waƙar baka daidai fahimtarsu. Ɗangambo (1982) ya bayyana waƙar baka da cewa; "Waƙa wani furuci (lafazi ko saƙo) ne cikin azanci da ake aiwatarwa ta hanyar rerawa da daidaita kalmomi cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da dabaru ko salon armashi".

A wata ma'anar kuwa an bayyana waƙar baka da cewa; "wani zance ne shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gava-gava bisa ƙa'idojin shiryawa da daidaitawa, a rere cikin sautin murya da amsa-amon kari da amshi da kiɗa" Gusau, (2008).

### 3.3.1 Ma'anar Makaɗa

Kalmar makaɗa kalma ce da aka samo ta daga 'kaɗa ko kiɗa ko kiɗi'. A nan kalmar na nufin waƙa tare da buga ko kaɗa wani abu domin samar da wani amo ko sauti na musamman. An yi wa kalmar kiɗa ƙarin ma'anar ta ma- a farkonta sai ta koma makaɗa. Ashe ke nan Makaɗa mutane ne da suke yin kiɗa da waƙa da fatar baki. Wannan ne ma ya sa ake kiransu makaɗan baka.

### 3.3.2 Rabe-Raben Makaɗa

Masana irin su Ɗangambo (1984) da Yahya (1984) da Gusau (2008) da sauransu sun karkasa makaɗa zuwa manyan rukunoni kamar haka:
- Makaɗan fada(sarauta)
- Makaɗan jama'a
- Makaɗan sha'awa
- Makaɗan ban dariya
- Makaɗan sana'a
- Makaɗan jarunta (maza)

### 3.3.3 Siffofin Waƙar Baka

Siffofin waƙar baka ta Hausa a bayyane suke, su waɗannan siffofi su ke bambanta waƙar baka da rubutatta, waɗannan sjiffofi sun haɗa da: waƙar baka ta Hausa na da tushe/gindin waƙa, waƙar kuma tana zuwa da kiɗa, ana kuma rereta. Akwai yan amshi da rawa kuma an gabatar da ita cikin ƙungiya. Waƙoƙin na da tsarin ɗiyan waƙoƙi masu sheɗara ko sheɗaru a kowane ɗan waƙa, akwai kuma rashin didaiton sheɗara ko sheɗaru da kuma rashi daidaito tsakani ɗa na farko da mai bi masa. Waɗannan siffofi ko shakka babu su ke bambanta waƙar baka ta Hausa da sauran nauoin waƙoƙin Hausa.

### 3.3.4 Kayan Kiɗa

A wurin Hausawa kiɗa wani muhimmin al'amari ne a cikin rayuwar Hausawa. Baya ga cin abinci da ibada da karatu, da wuya a samu wani abu da Bahaushe yake yi wanda babu kiɗa a cikinsa. (Gusau, 2008). Misali, Manoma suna da makaɗansu musamman ma lokacin aikin gayya, mata a cikin gida, musamman lokacin ayyukan gida kamar niƙa da daka da raino duk akwai nau'ukan amo da suke haɗawa da shi. Fatake a lokacin tafiya sukan tafi da makaɗansu domin ɗebe masu kewa.

Mayaƙa a fagen yaƙi suna da kayan kiɗansu kamar kuge da kurya gangan mutuwa da tambari da sauransu. (Gusau, 2008).

An raba kayan kiɗan Hausawa zuwa manyan rukunai huɗu kamar haka;
1- Ganguna
2- Kayan izga ko tsarkiya
3- Kayan bushe-bushe
4- Sauran kayan kiɗa

**1 – Ganguna**

Da yawa cikin kayan kiɗan da ke cikin wannan kason sukan kasance an rufa su ne da fata, wanda ake buga fatar domin samar da amon kiɗa. Misalin kayan kiɗan da ke wannan rukuni sun haɗa da: Ganga da Jauje da dundufa da kurya da talle da turu da kalangu da ɗan karvi da duma da tambari da taushi da duman girke da kotso da kwairama da banga da tallabe da ƙoroso da sauransu

**2 - Kayan Isga ko Tsarkiya**

Waɗannan sun haɗa da: Garaya da goge da kuntigi da gurmi da kukuma da kumbo da kumsa da sauransu.

**3 – Kayan Bushe- bushe**

Waɗannan sune kayan kiɗan Hausawa waɗanda ake hurawa da baki domin samar da amo. Misalansu sun haɗa da: Algaita da farai da kakaki da damalgo da ƙaho da sarewa da bututu da tilliveri da kwagira da sauransu.

**4- Sauran kayan kiɗa**

A wannan kason an kawo sauran abubuwan Hausawa ke samar amon kiɗa da su ne baki ɗaya, waɗanda ba su cikin sauran kason da aka kawo a baya. Waɗannan kayan kiɗa sun haɗa da: Tafin hannu da farankace da shantu da sakaina da kacakaura da gwangwani da ƙwarya da buta da zunguru da ɗuwawu da dutsen nika da akayau da zuga-zugi da sauransu. Waɗannan da ma wasu su ne kayan kiɗan da Hausawa ke amfani da su.

Auna Fahimta

1. Bayyana siffofin waƙar Baka waɗanda suka bambantata da sauran nau`o`in waƙoƙin Hausa.
2. An raba kayan kiɗan Hausawa zuwa manyan rukunai huɗu. Kawo su.

## 3.5 Taƙaitawa

A cikin wannan kashi an kawo bayanai ne kan waƙar baka, inda a ciki aka kawo ma'anar waƙar baka da siffofinta da ma'anar makaɗa da rabe-rabensu. Haka kuma an kawo bayani kan kayan kiɗan Hausawa.

## 3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Kayan Isga ko Tsarkiya**:** Waɗannan sun haɗa da: Garaya da goge da kuntigi da gurmi da kukuma da kumbo.

Makaɗa: **-** kalma ce da aka samo ta daga 'kaɗa ko kiɗa ko kiɗi'. A nan kalmar na nufin waƙa tare da buga ko kaɗa wani abu domin samar da wani amo ko sauti na musamman

## 3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Bayyana siffofin waƙar Baka waɗanda suka bambantata da sauran nau`o`in waƙoƙin Hausa.

i- Waƙar baka ta Hausa na da tushe/gindin waƙa,

ii- waƙar kuma tana zuwa da kiɗa,

iii- ana kuma rereta.

iv- Akwai yan amshi da rawa kuma an gabatar da ita cikin ƙungiya.

v- Waƙoƙin na da tsarin ɗiyan waƙoƙi masu sheɗara ko sheɗaru a kowane ɗan waƙa,

vi- akwai kuma rashin didaiton sheɗara ko sheɗaru da kuma rashi daidaito tsakani ɗa na farko da mai bi masa.

2- An raba kayan kiɗan Hausawa zuwa manyan rukunai huɗu. Kawo su.

i- Ganguna

ii- Kayan izga ko tsarkiya

iii- Kayan bushe-bushe

iv- Sauran kayan kiɗa

# KASHI NA HUƊU ZUBE NA BAKA

**Abubuwan da suke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Zube na baka
4.3.1 Hausawa Bayan Ruwan Ɗufana
4.3.2 Harshen Hausa Bayan Ruwan Ɗufana
Auna Fahimta
4.3 Taƙaitawa
4.4 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.5 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan zube na baka, wato zuben da ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka, musamman abin da ya shafi ƙirƙirarrun labarai da suka haɗa da tatsuniya da hikaya da ƙissa da kuma almara.

## 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma'anar zube na baka da ƙirƙirarrun labarai
- Rarrabe nau'o 'i da misalan zube na baka
- Fayyace yadda nau'o'i da misalan zuben suka kasance na baka
- Bayyana ma'anonin wasu nau'o'in zube na baka

## 4.3 Ma'anar Zube

Zube nau'i ne na adabi da yake nufin wata hikima, ko basira ko tunani irin na ɗan'Adam da ya ƙaga kan wani abu, ya furta da fatar baki domin watsa wata manufa don koyarwa ko kuma hannunka-mai-sanda da jagora don nishaɗi. Akwai ire-iren waɗannan zube da yawan gaske a cikin adabin Hausa da suka haɗa da ƙissa da tarihi ko tarihihi da

tatsuniya da almara da hikaya da zaurance da salon magana da kirari da take da zambo da sauransu da dama.

Haka kuma ana iya kallon zube na baka da zance na hikima da ake shiryawa cikin azanci da yake zuwa a kara zube, wani lokacin kuma mai ɗan tsawo, mai kuma ban sha`awa da koyar da dabarun zaman duniya ta hanyoyi da matakai daban-daban. Kenan, ana iya bambanta zube da waƙa da wasan kwaiwayo ta fuskar adabi, wato ana iya cewa a waƙa da wasan kwaikwayon sai an tsara, an kuma shirya, sa'annan kuma a daidaita tunani kafin a aiwatar da su alhali kuwa a zube ba a buƙatar waɗannan abubuwa.

### 4.3.1 Ma'anar Ƙirƙirarrun Labarai

Ƙirƙirarrun labarai zance ne na hikima da ake shiryawa cikin azanci da suke zuwa a kara zube, kuma mai ɗan tsawo, mai kuma ban sha`awa da koyar da dabarun zaman duniya ta hanyoyi da matakai daban-daban. Irin waɗannan ƙirƙirarrun labarai galibi suna da tsayi. Misali tatsuniya da hikaya da ƙissa da almara, da sauransu.

### 4.3.2 Tatsuniya

Tatsuniya tana daga cikin manyan rasa na adabin bakan Bahaushe, kuma ƙagaggen labari ne da Bahaushe kan ba `ya`yansa domin su tashi cikakku kuma kamilan mutane.
Masana da dama sun daɗe suna kallon tatsuniya ta fuskoki daban-daban, (Gusau, 2006) cewa yake "tatsunniya wani tsararren labari ne wanda magabata (musamman tsofaffin mata) suke shiryawa cikin hikima da nuna ƙwarewa da naƙaltar harshe da ya ƙunshi wata shiryarwa da nuni zuwa ga halaye da ilmin zaman duniya, sannan da saka nishaɗi da raha ga rayuwa da kuma cinye dare".

Saboda haka tatsuniya makaranta ce ta malam Bahaushe, ta nan yakan ilimantar da `ya`yansa dabarun zaman duniya tun kafin Bahaushe ya sadu da baƙi. Ta amfani da tatsuniya Bahaushe kan kaifafa tunanin `ya`yansa. Saboda haka, tsofaffi ne kan shirya tatsuniya, kuma ƙirƙirarren labari ne da akan shirya domin ilmantarwa ga yara. Ana buɗe tatsuniya ne da 'Gatanan gatananku' a rufe kuma da 'Ƙurungus'. Galibi an fi yin tatsuniya da dare, in kuwa za a yi da rana to sai an ɗaure gizo.

### 4.3.3 Hikaya

Hikaya labari ne da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma ƙwari. Wani lokaci kuma takan ɗauki yanayin ƙago wasu labaran don ƙarin bayani kan wani abu ko kwaikwayon sa. Hikaya labari na manyan

mutane, ba annabawa ba, da abin da ya faru gare su. Misali, hikayar wani halifa ko sahabi ko wani babban sarki. Hikaya kuma, takan ƙunshi wani abin mamaki da ya auku ko kuma dai wani labari mai koya darasi ga zaman duniya (ko ma amfanin lahira). Hikaya kuma tana iya zama ta wani attajiri ko kuma dai wani labari mai koya zaman duniya dangane da yadda mutum zai iya bakinsa, (Ɗangambo, 2008).

### 4.3.4 Ƙissa

Ƙissa labari ne na gaskiya da aka bayar ko ake bayarwa a kan rayuwar annabawa da sahabbai ko waliyyai ko shaihunnan malamai, ko wasu bayin Allah da sauran su da suka danganci addinin Musulunci, musamman waɗanda Alƙur'ani da Hadisai suka kawo bayaninsu.

Hausawa sun sami damar sanin wani labari da ake kira da suna 'ƙissa' bayan cuɗanyarsu da Larabawa, suka kuma samu damar rabauta da addinin Musulunci. Don haka a iya cewa tasirin addinin Musulunci da karance-karancen da suka danganci tafsiri da hadisai da wa'azi wajen watsa addinin Musulunci, su ne suka taimaka wajen samuwar ƙissa a al'ummar Hausawa.

Masana da dama sun raba ƙissa zuwa sassa daban-daban. Daga cikin su akwai Sa'idu Muhammad Gusau wanda ya kasa ƙissa zuwa nau'i huɗu kamar haka:

- Ƙissar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).
- Ƙissar Sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke ƙunshe da bayanin rayuwarsu.
- Ƙissar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miƙa wuyansu ga addinin Allah.

Ƙissar kangararru, waɗanda suka bijire wa addinin Allah.

### 4.3.5 Almara

Almara ita ce hanyar gabatar da wasu matsaloli kara-zube ko kuma ta hanyar labari, sannan a buƙaci mai sauraro ya bayar da amsa ko kuma ya zava tsakanin abubuwan da aka ambata. Gusau, (1995), yana ganin almara wani shiryayyen labari ne na jawo hankali da ake bayarwa don kaifafa tunanin masu sauraro ko nishaɗi. Saboda haka almara ba ta fiye tsawo sosai ba; sai dai takan ƙunshi wani abu na ban dariya ko ƙalubalen da za a nemi mai sauraro ya warware. A taƙƙaice, almara labari ne ƙirƙirarre wanda ba lalle ne ya auku ba.

Tun kafin Hausawa su haɗu da Larabawan suna da ire-iren waɗannan labaru na ban dariya da sa nishaɗi. Misalin almara ta kaifafa tunani mai buƙatar sai an yi tunani kafin a bayar da amsa, ita ce; wasu adadin tsuntsaye ne a sama da kuma wasu a ƙasa. Sai na sama suka cewa na ƙasa da ɗaya daga cikinku zai hawo sama da adadinmu ya zama ɗaya. Su kuma na ƙasa suka ce wa na sama da ɗaya daga cikinku zai sauko ya haɗu da mu da adadinmu ya ninka naku. Shin tsuntsaye nawa ne a sama kuma nawa ne a ƙasa?

Auna Fahimta

1 Kawo nau'o'in zube na baka guda biyar (5)

2 Tatsuniya tana daga cikin manyan rasa na _______

## 4.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an tattauna a kan zube na baka, wato zuben da ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka, musamman abin da ya shafi ƙirƙirarrun labarai. Kashin ya ƙunshi ma'anar zube da ma'anar ƙirƙirarrun labarai da kuma ma'anoni na wasu daga cikin misalansu da suka haɗa da tatsuniya da hikaya da ƙissa da kuma almara.

## 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Ƙissar Annabawa: - ƙissa ce wadda ake bayyana rayuwar Annabawa ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).

Hikaya labari : - shi ne labarin da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma ƙwari

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Kawo nau'o'in zube na baka guda biyar (5)

- ƙirƙirarren labari

Tatsuniya
Hiƙaya
Almara
ƙissa

# KASHI NA BIYAR WASANNIN KWAIKWAYO

## Abubuwan da suke Ciki

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufofin Darasi
5.3 Ma'anar Wasa
  5.3.1 Ma'anar Wasan kwaikwayo
  5.3.2 Bambancin Wasa da Wasan Kwaikwayo
  5.3.3 Ire-Iren Wasannin kwaikwayon gargajiya
  Auna Fahimta
5.4 Taƙaitawa
5.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 5.1 Gabatarwa

Wannan darasi yana bayani akan wasannin kwaikwayo na gargajiya, ba za a iya kintacen lokacin da Hausawa suka fara waɗannan wasannin ba. Abin da ya fi karvuwa ga masana da manazarta shi ne wasanni ne da aka gada tun kaka da kakanni, masu gudanar da waɗannan wasannin galibi matasa ne da kuma yara maza da mata. Akwai wasannin da suka samu sanadiyyyar shigowar addinin musulunci kamar wasannin tashe, sauran kuwa wasanni ne da tun da daɗewa ake yin su a cikin al`umma.

## 5.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- wasannin da Hausawa suke da su tun kafin su yi cuɗanya da wasu al`ummomi.
- Muhimmin abu da kan a iya bambancewa tsakanin wasa da wasan kwaikwayo.

## 5.3 Ma’anar Wasa

Shi dai wasa na nufin duk abin da ba gaskiya ba, yana kuma ɗauke da raha da ban dariya da nishaɗI ko annashuwa a magance ko a aikace. A wasu wuraren, wargi shi ake nufi da wasa, a waɗansu wuraren kuwa, wargi na nufin mugun wasa ne.,

### 5.3.1 Ma’anar Wasan Kwaikwayo

Wasan kwaikwayo adabi ne mai bayyana hikima da fasahar al’umma. Haka kuma hanya ce wadda take nuna hoton rayuwar al’umma. Tamkar yadda idan mutum ya duba madubi zai iya ganin kansa a ciki, haka ma za a iya ganin hoton rayuwar al’ummar da suka gabata ta hanyar wasan kwaikwayonta. Za a iya ganin hoton abin da ke faruwa a cikin al’umma, har ma wani lokaci a iya ƙirdaden abin da zai kai-komo cikin al’umma. Hanya ceta bayyana ko dai tunanin mai shirya wasan, ko marubuci, ko kuma irin falsafarsa game da rayuwa. Abrams, (1953).

Kalmomi guda biyu suka haɗu don bayyana ma`anar wasan kwaikwayo, wato akwai wasa akwai kuma kwaikwayo, wanda ke nuni da aikata wanin abu don kwatanta yadda yake, ko yadda ake yin sa, ko don a ga kyansa ko kuma muninsa.

Kwaikwayo a matsayinsa na wani ginshiƙi wanda ɗan Adam yake amfani da shi wajen gudanar da rayuwarsa ta yau da kullum ya yi kaka-gida a mafi yawa daga cikin wasannin Hausawa. A nan ana buƙatar yin wata matashiya, kalmar ‘Drama’ a dunƙule kamar yadda aka santa kuma ga masu nazarinta na nufin wasannin kwaikwayo waɗanda aka rubuta domin a awaitar a dandamali a gaban masu kallo. Ire-iren waɗannan wasanni ko kuma a ce nau’o’in waɗannan wasanni ba su wuce waɗanda suka yi fice na raha da ban tausayi da tir-madalla da dai sauransu ba.

Masana da dama sun bayyana ma`anar wasan kwaikwayo ta fuskokin da suka fahimci lamarin. Mashahurin malamin falsafar nan wato Aristotle, (1996) ya bayyana wasan kwaikwayo da cewa ‘kwaikwayon wani aiki ne, haka kuma kwaikwayon wani mutum ko mutane ta hanyar kwatanta yadda suke yin wani aiki.

Crow, (1983:4) ya bayyana ma`anar was an kwaikwayo da cewa wani rin wasa ne a inda mutane kan kwaikwayi wasu mutane ko wasu abubuwa dangane da halayensu ko irin abubuwan da suke gudanarwa, ana yin wannan was an ne domiun nishaɗantarwa ga masu kallo.

Shi kuwa Kofoworola, (1977:3) a taƙaice cewa ya yi wasan kwaikwayo wata fasaha ce wadda ke samar da jin daɗi da annashuwa ga rayuwar ɗan Adam.

Yahaya, (1978:244) ya ce ai wasan kwaikwayo, ko da jin sunansa ma ya riga ya bayyana kansa, wato akwai alamar wasa watau abin da yake raha, akwai kuma alamun kwaikwayo, wato aikata wani abu don kwatanta yadda ake yin shi.

A dunƙule wasan kwaikwayo, kwaikwayon wani abu ne ta fuskar wasa, inda harhaɗuwar wasu ayyukan ‘yan wasa kan samar da cikakken labari don isar wa ga al’umma. Wannan labari mai ɗauke da wata manufa kan iya kasancewa ya faru cikin al’umma ko kuma ƙirƙirarsa kawai aka yi.

Idan an lura da duk bayanan da aka kawo kan ma’anar wasan kwaikwayo sai a taras ma’anar ta ƙunshi abubuwa da dama. Da farko dai bayan bayyana ma’anar da ake son a gane na shi kanshi wasan kwaikwayon, an haɗa har da irin saƙon da ake fatar wasannin su isar ga al’umma. Haka kuma wasu bayanan sun ɗan yi nuni da ire-iren wasan kwaikwayo ko da kuwa ba su faɗaɗa ba.

### 5.3.2 Bambancin Wasa da Wasan Kwaikwayo

Shi dai wasa na nufin duk abin da ba gaskiya ba, yana kuma ɗauke da raha da ban dariya da nishaɗi, akwai kuma kwaikwayo, wanda ke nuni da aikata wanin abu don kwatanta yadda yake, ko yadda ake yin sa, ko don a ga kyansa ko kuma muninsa.

| **Wasa** | **Wasan Kwaikwayo** |
|---|---|
| Ana yi don raha | Koya darussa |
| Ba kwaikwayo | Akwai kwaikwayo |
| Ba Sauya kamanni | Akwai Sauya kamanni |
| Badole don a gani ba | A dandali don a gani |
| ukar lokaci mai tsawo | Ana ɗaukar lokaci mai |
| tsawo | |
| Ba wani lokaci tsayayye | Akwai lokutan gabatar |
| da shi | |

### 5.3.3 Ire-Iren Wasannin kwaikwayon gargajiya

**i- Tashe**

Tashe yana ɗaya daga cikin wasannin gargajiya da ake gudanarwa a ƙasar Hausa, domin idan muka ga yadda ake gabatar da shi za mu ga cewa akwai wasu ɗabi’u da tarbiyya ta yau da kullum waɗanda suka shafi rayuwar Hausawa. Masana ilmi sun bayar da ma’anonin tashe kamar haka : -

Ahmed (1985 :8) ya ce: ‘ Tashe a kowane bangaren ƙasar Hausa ana yin shi ne a watan azumi, lokacin watan ya kai kwana goma, dalilai uku suka haifar da tashe, na farko don a tashi jama’a lokacin sahur, kamar yadda kalmar nan “tashe” ta nuna. Dalili na biyu shi ne, don hana mutane wasanni almubazzaranci, na uku ana yin wasannin tashe ne domin nishaɗi bayan buɗe baki’.

Shi kuma Umar (1980 :3) ya ce: ‘tashe al’ada ce da aka yi a cikin watan nan mai alfarma wato watan Ramalan. A wannan wata Ubangiji Tabaraka Wata’ala ya umarci Musulmi da yin azumi, ya kuma kwaɗaitar da su ga yawaita ayyukan Ibada. Don haka, za mu iya cewa tashe wasa ne da ke ɗauke da nishaɗi da nuna farin ciki a wani ƙayyadadden lokaci da yara maza da ‘yan mata da samari ke gudanarwa”.

Dangane da ire-iren tashe, masana ilimi irin su Ahmed, da Umar, sun karkasa tashe na yara maza zalla da tashen ‘yan mata da kuma tashen Samari matasa.

**(1)** **Tashen yara maza, sun haɗa da:** Sakanni-in ɗiba, ka-yi -rawa, da Ɗan duƙununu, da Tsoho da gemu, da Danda dokin kara, da Zan buga, kar-ka buga, da Tashi wali da dai sauransu.

**(2)** **Tashen yan mata sun haɗa da:** Samodara, da Maryama da Daudu, da Asha ruwa, da Mai ciki, da Auren-gidan-sharu-ba-dadĪ da dai sauransu.

**(3)** **Tashen Samari :** Sun haɗa da Amale mai Jan-kaya, da Jatau mai magani, da Gwauro ya tsinke, da Kai ni, chadi zan tafi da Macukule da dai sauransu.

**ii- ’Yankamanci**

`Yankamanci wasa ne na ban dariya inda ɗan kama kan sa buje da baban riga da takobin ice dad a tasbahan ƙuli-ƙuli da gangar sakaina. Yakan kwave babar rigarsa don ya yi ƙunzugu da ita ta hanyar cusa ta cikin wandonsa. Duk maganar ɗan kama bat a wuce ta abinci, ko day a yi wata Magana wadda ta shafi addini za a taras ya sauya mata tsari ta koma maganar abinci. Idan ya sami fitacciyar waƙar wani sai ya sauya mata kalmomin dake ciki don ta koma siagar abinci. Yakan yi amfani da kayayyakin da aka lissafa a sama musamman takobi don kai hari na barazana. Wata siffa taɗ an kama it ace ba ya karvar kyauta da hannu sai dai a jefa masa inda shi kuma zai café da baki.

**iii- Kalankuwa**

Hausawa sun daɗe da sanin wasan kwaikwayo da kuma gudanar da shi a wasu lokutan gudanar da bukukuwan wasannin gargajiyansu. Masana na ganin abin da aka fi sani da suna wasan kwaikwayo (Drama) asali ana kiransa wasan gauta ne. Yahaya da Muhammad, (1978). Wasan gauta ya kasu kashi biyu, akwai wanda ake yi a fada wanda ƙwaraƙwaran sarki ke yi, da kuma wanda samari da ‘yan mata suke haɗuwa a Dandali (wuri na

musanman don gudanar da wasanni). Dukkan su iri ɗaya ne sai dai wanda ake yi a fada, galibi Sarki da Hakimansa da iyalansa ne ‘yan kallo, wanda samari ke shiryawa kuwa kowa da kowa na iya zuwa ya kalla. Akan shirya wasan ne ta kwaikwayon harkokin mulki da gudanar da shari’a a karkara cikin Kaka. Dagacin garin shi ne kan naɗa sarkin samari. Shi kuma sarkin samari shi ne zai naɗa mataimakansa kamar su Galadima da Madaki da Waziri da Alƙali.

A wasu wurare irin wannan da ake aiwatarwa a cikin garur-ruwa ko ƙauyuka ba tare da an fita zuwa wani wuri ba shi ne wasan Kalankuwa. Idan an sami fita ziyartar wasu ƙauyuka ko garurruwa, nan ne ake masa laƙabi da wasan Magi. Muhammad da Yahaya, (1978).

Wasu kuwa gani suke wasan Kalankuwa na cikin bukukuwan Hausawa na gargajiya wanda ake gudanarwa shekara-shekara. Masu shirya wasan kan gudanar da zaɓe a tsakaninsu tukun kafin a shiya wasan. Samari da ‘yan mata ke zaɓen waɗanda za su shugabanci gudanar da wasan da kuma al’amurarsu. Sarakunan ƙauyuka da garurruwa su suke tabbatar da wannan zaɓe na samarin ta naɗa mutane da samarin suka zaɓa. Irin wannan sarautu sun haɗa da Sarkin samari da Sarauniyar ‘yan mata da Alƙalin samari da Sarkin dogaran samari da Yari da sauransu. Ibrahim, (1982).

A yayin da wasu suke yin masa wannan kallon, wasu kuwa gani suke Wasan Kalankuwa *“Tumbin Giwa”* ne ko kuma a ce *“Jakar Magori”* ce inda ake samun harhaɗuwar wasanni da dama a lokacin da ake gudanar da wasan. Mai wannan ra’ayi ne kuma yake ganin a wasu wurare maimakon a kira wasan da Kalankuwa, shi ake kira da *Wasan Magi* ko *Wasan gauta.* Akan aiwatar da *Wasan gauta* ne a matsayin ɗaya daga cikin wasannin da ake aiwatarwa a lokacin gudanar da *Wasan Kalankuwa,* Ahmed, (1985).

| | |
|---|---|
| 1- | Zaɓi biyu daga waɗannan a bayyana yadda suke:<br>- Tashe<br>- `Yankamanci<br>- Kalankuwa |
| 2- | wasa ne na ban dariya inda ɗan kama kan sa buje da baban riga da takobin ice dad a tasbahan ƙuli-ƙuli da gangar sakaina. |

## 5.4 Taƙaitawa

Darasin nan ya yi bayanin muhimman abubuwa da suka ƙunshi: Ma`anar wasan kwaikwayo na gargajiya da ma`anar wasa, bambancin wasa da wasan kwaikwayo ma a duba shi, an kuma yi bayanin yadda ake gudanar da wasu daga ciki a matsayin misalai. Wasan tashe, wasa ne wanda ya samu sanadiyyar shigowar addinin musulunci, shi kuwa wanan `Yangambara da kalankuwa ta sauran wasnnin itrin su danad dokin kara da was an tuwon ƙasa da na `yar tsana duk wasaannin kwaikwayon gargajiya ne waɗanda sai a darasi na gaba za a duba su.

## 5.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Ƙissar Annabawa: - ƙissa ce wadda ake bayyana rayuwar Annabawa ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).

Hikaya labari : - shi ne labarin da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma ƙwari

## 5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Zaɓi biyu daga waɗannan a bayyana yadda suke:

i- Tashe

Tashe yana ɗaya daga cikin wasannin gargajiya da ake gudanarwa a ƙasar Hausa, domin idan muka ga yadda ake gabatar da shi za mu ga cewa akwai wasu ɗabi'u da tarbiyya ta yau da kullum waɗanda suka shafi rayuwar Hausawa. Tashe a kowane bangaren ƙasar Hausa ana yin shi ne a watan azumi, lokacin watan ya kai kwana goma, dalilai uku suka haifar da tashe, na farko don a tashi jama'a lokacin sahur, kamar yadda kalmar nan "tashe" ta nuna. Dalili na biyu shi ne, don hana

mutane wasanni almubazzaranci, na uku ana yin wasannin tashe ne domin nishaɗi bayan buɗe baki'.

ii- `Yankamanci

`Yankamanci wasa ne na ban dariya inda ɗan kama kan sa buje da baban riga da takobin ice dad a tasbahan ƙuli-ƙuli da gangar sakaina. Yakan kwave babar rigarsa don ya yi ƙunzugu da ita ta hanyar cusa ta cikin wandonsa. Duk maganar ɗan kama bat a wuce ta abinci, ko day a yi wata Magana wadda ta shafi addini za a taras ya sauya mata tsari ta koma maganar abinci. Idan ya sami fitacciyar waƙar wani sai ya sauya mata kalmomin dake ciki don ta koma siagar abinci. Yakan yi amfani da kayayyakin da aka lissafa a sama musamman takobi don kai hari na barazana. Wata siffa taɗ an kama it ace ba ya karvar kyauta da hannu sai dai a jefa masa inda shi kuma zai café da baki.

iii- Kalankuwa

Hausawa sun daɗe da sanin wasan kwaikwayo da kuma gudanar da shi a wasu lokutan gudanar da bukukuwan wasannin gargajiyansu. Masana na ganin abin da aka fi sani da suna wasan kwaikwayo (Drama) asali ana kiransa wasan gauta ne. Yahaya da Muhammad, (1978). Wasan gauta ya kasu kashi biyu, akwai wanda ake yi a fada wanda ƙwara ƙwaran sarki ke yi, da kuma wanda samari da 'yan mata suke haɗuwa a Dandali (wuri na musanman don gudanar da wasanni). Dukkan su iri ɗaya ne sai dai wanda ake yi a fada, galibi Sarki da Hakimansa da iyalansa ne 'yan kallo, wanda samari ke shiryawa kuwa kowa da kowa na iya zuwa ya kalla. Akan shirya wasan ne ta kwaikwayon harkokin mulki da gudanar da shari'a a karkara cikin Kaka. Dagacin garin shi ne kan naɗa sarkin samari. Shi kuma sarkin samari shi ne zai naɗa mataimakansa kamar su Galadima da Madaki da Waziri da Alƙali.

A wasu wurare irin wannan da ake aiwatarwa a cikin garur-ruwa ko ƙauyuka ba tare da an fita zuwa wani wuri ba shi ne wasan Kalankuwa. Idan an sami fita ziyartar wasu ƙauyuka ko garurruwa, nan ne ake masa laƙabi da wasan Magi

2-____wasa ne na ban dariya inda ɗan kama kan sa buje da baban riga da

takobin ice dad a tasbahan ƙuli-ƙuli da gangar sakaina.

- `Yankamanci

## RUKUNI NA UKU Adabin Zamani


| | |
|---|---|
| Kashi Na 1 | Ma’anar Adabin Zamani |
| Kashi Na 2 | Ire-Iren Adabin Zamani |
| Kashi Na 3 | Rubutacciyar Waƙa |
| Kashi Na 4 | Rubutaccen Zube |
| Kashi Na 5 | Rubutaccen Wasan Kwaikwayo da Adabin Radiyo da na Talbijin |


## KASHI NA ƊAYA MA’ANAR ADABIN ZAMANI

### Abubuwan da Suke Ciki


1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Ma’anar Adabin Zamani
 1.3.1 Ma’anar Zamani
 1.3.2 Siffofin Adabin Zamani
 1.3.3 Ire-Iren Adabin Zamani
 Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta




### 1.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan adabin zamani, wato adabin da ya wanzu bayan Bahaushe ya sami hanyar rubutu da karatu sakamakon haɗuwa da baƙin al’ummu. A wannan gavar za a bayyana ma’anar adabin zamani, sai kuma ma’ana da siffofi da ire-iren adabin zamani.



### 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma’anar adabin zamani
- Siffofin adabin zamani
- Ire-iren adabin zamani

## 1.3 Ma’anar Adabin Zamani

Adabin zamani kamar yadda sunansa ya nuna, adabi ne da zamani ya kawo. Wato adabi ne da ya wanzu bayan Hausawa sun koyi karatu da rubutu sakamakon zuwan Larabawa da Turawa ƙasar Hausa. Ana kiran sa rubutaccen adabi saboda ana tsara shi da wanzar da shi a rubuce. Kenan, hanyar wanzar da adabin zamani(rubutu) ita ce ta bambanta shi da adabin gargajiya ko na baka.

### 1.3.1 Ma’anar Zamani

Ƙamusun Hausa na Jami’ar Bayero (2006), an bayyana ma’anar zamani da cewa “lokacin da ake ciki mai ci.” Zamani ne ke shigowa da wasu ƙaƙale- ƙaƙale da suka sauya da waɗanda aka saba da su. Wato idan muka duba wannan bayani za mu ga ai zamani ne yake shigowa da wasu abubuwan da babu su a da can, idan zamani ya zo da wani abu ko kuma baƙon abu da ya zo wa mutane sabo ga wani lokaci ko wani zamani domin tafiyar da harkokinsu na yau da kullum.

Saboda haka, duk inda aka kai aka kawo, ma’anar zamani ba ta wuce lokacin da ake ciki ba, wannan ya haɗa da yayi da fasalce-fasalcen tsarin rayuwar yau wanda ke ɗamfare da zamananci ko tasirin baƙin al’adu cikin al’adun da aka saba da su. Zamani a ƙasar Hausa ya zo da cuɗanyar al’adu na wasu al’umma, kuma ya yi naso sosai a al’adun Hausawa musamman da suka shafi sutura da aure da haihuwa da siyasa da kasuwanci da zamantakewa.

Har ila yau zamani ne ke shigowa da wasu ƙaƙale- ƙaƙale da suka sauya da waɗanda aka saba da su. Wato idan muka duba wannan bayani za mu ga ai zamani ne yake shigowa da wasu abubuwan da babu su a da can, idan zamani ya zo da wani abu ko kuma baƙon abu da ya zo wa mutane sabo ga wani lokaci ko wani zamani domin tafiyar da harkokinsu na yau da kullum.

### 1.3.2 Siffofin Adabin Zamani

Ba tare da an tsawaita ba, akwai siffofin da suka kevanta ga adabin zamani kuma su ne suka bambanta shi da adabin gargajiya. Siffa ta farko kuma mafi muhimmanci ita ce rubutu. A taƙaice, adabin zamani yana da waɗannan siffofi:

- Ana ƙirƙirar shi a ka, a wanzar a rubuce
- Ana adana shi a rubuce
- Akan gabatar a rubuce ko ta baka ko a aiwatar
- Adabi ne mai ƙunshe da tasirin baƙon tunani musamman na Larabawa da Turawa

- Bahaushe ya koyi tsarawa da wanzar da adabin zamani ne daga baƙin al'ummu, wato Larabawa da Turawa.

### 1.3.3 Ire-Iren Adabin Zamani

Adabin zamani ya kasu gida uku, akwai rubutacciyar waƙa da rubutaccen zube da kuma wasannin kwaikwayo na zamani. Kowanne daga cikin waɗannan akwai nau'o'insu da suka kevanta ga kowane kasha. Misali, wasannin kwaikwayo na zamani ya ƙunshi na rediyo da na talabijin da rubutacce na littafi da fina-finai da sauransu.

Auna Fahimta

1. Bayyana ma'anar adabin zamani
2. Kawo ire-iren adabin zamani

## 1.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an kawo bayanai kan adabin zamani, wato adabin da ya wanzu bayan Bahaushe ya sami hanyar rubutu da karatu sakamakon haɗuwa da baƙin al'ummu. An tattauna ma'anar adabin zamani, sai kuma ma'ana da siffofi da ire-iren adabin zamani.

## 1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Adabin zamani: - adabi ne da ya wanzu bayan Hausawa sun koyi karatu da rubutu sakamakon zuwan Larabawa da Turawa ƙasar Hausa.
Zamani: - lokaci

## 1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 1.7 **Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar adabin zamani

Adabin zamani kamar yadda sunansa ya nuna, adabi ne da zamani ya kawo. Wato adabi ne da ya wanzu bayan Hausawa sun koyi karatu da rubutu sakamakon zuwan Larabawa da Turawa ƙasar Hausa. Ana kiran sa rubutaccen adabi saboda ana tsara shi da wanzar da shi a rubuce. Kenan, hanyar wanzar da adabin zamani(rubutu) ita ce ta bambanta shi da adabin gargajiya ko na baka.

2. Kawo ire-iren adabin zamani

Adabin zamani ya kasu gida uku,

i- akwai rubutacciyar waƙa

ii- rubutaccen zube

iii- wasannin kwaikwayo na zamani.

# KASHI NA BIYU RABE-RABEN ADABIN ZAMANI

## Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Adabin zamani
2.3.1 Rubutacciyar Waƙa
2.3.2 Rubutacciyar Zube
2.3.3 Rubutaccen Wasan Kwaikwayo
2.3.4 Adabi Na Rediyo
2.3.5 Adabi Na Talbijin
2.3.6 Adabi Na Yanar Gizo
Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 2.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan ire-iren adabin zamani, wato adabin da wanzu bayan zuwan Larabawa da Turawa ƙasar Hausa. A wannan gavar za a kawo bayanin ire-iren adabin zamani waɗanda suka haɗa da rubutacciyar waƙa da rubutaccen zube da rubutaccen wasan kwaikwayo da adabi na rediyo da na talabijin da kuma na yanar gizo.



## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Rabe-rabe adabin zamani
- Ma'anar rubutacciyar waƙa
- Ma'anar rubutaccen zube
- Ma'anar rubutaccen wasan kwaikwayo
- Ma'anar adabi na rediyo da na talabijin da na yanar gizo

## 2.3 Rabe-Raben Adabin Zamani

Adabin zamani ya ƙunshi rubutacciyar waƙa da rubutaccen zube da rubutaccen wasan kwaikwayo da adabi na rediyo da na talabijin da kuma na yanar gizo.

### 2.3.1 Rubutacciyar Waƙa

Rubutacciyar waƙa wani saƙo ne da ake gina shi a kan tsararriyar ƙa'ida ta baiti da ɗango da kari da amsa-amo da sauran ƙa'idojin da suka danganci daidaita kalmomi, da zavar su, tare da yin amfani da su, a rubuce sannan a rera lokacin da ake buƙata. (Sarvi, 2007: 10). Kenan, rubutacciyar waƙa ba kamar waƙar baka ba, ita a rubuce ake tsara ta kuma ba a rera ta da kiɗa kuma tana da tsarin baitoci da amsa-amo waɗanda tasiri ne na rubutattun waƙoƙin Larabawa, tun da daga gare su ne aka koyi rubuta waƙoƙi. An fara samun rubutattun waƙoƙi cikin ajami tun a ƙarni na 15 zuwa na 17, sai dai sun fi tashe cikin ƙarni na 19 sakamakon jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo inda aka yi amfani da waƙoƙi wajen isar da saƙonnin addinin Musulunci. Daga ƙarshen ƙarni na 19 zuwa farkon ƙarni na 20 aka cigaba da samar da rubutattun waƙoƙi cikin rubutun boko.

### 2.3.2 Rubutacciyar Zube

Rubutaccen zube nau'i ne na zube da ake tsarawa, a wanzar a kuma adana a rubuce. Rubutaccen zube nau'in zube ne da ya samu bayan Bahaushe ya iya karatu da rubutu, karatu da rubutu a wajen Bahaushe kuwa sun samu ne bayan haɗuwa da baƙin al'ummu musamman Larabawa inda ya sami rubutun ajami da kuma Turawa inda ya koyi rubutun boko. Bayan iya karatu da rubutu ne Bahaushe ya sami nau'in rubutaccen zube cikin siffar rubutaccen labari, abin da aka kira ƙagaggen labari a da, (Malumfashi, 2009 & 2018).

Rubutun zube ya ƙunshi abin da ya shafi adabi, misali rubutaccen labari da kuma abin da ba za a kira shi adabi ba misali rubuce-rubucen tarihi da siyasa da sauransu.

### 2.3.3 Rubutaccen Wasan Kwaikwayo

Ma'anar wasan kwaikwayo a Hausa a bayyane take daga lura da kalmomin da suka gina shi, wato abu ne mai alamun wasa da kuma kwaikwayo. Shi dai wasa na nufin duk abin da ba gaskiya ba, yana kuma ɗauke da raha da ban dariya da nishaɗi, akwai kuma kwaikwayo, wanda ke nuni da aikata wani abu don kwatanta yadda yake, ko yadda ake yin

sa, ko don a nuna kyawunsa ko kuma muninsa. Saboda haka [angambo (2008) ya ce "wasan kwaikwayo kamar yadda sunansa ya nuna, wasa ne da ake gina kan kwaikwayon wani labari ko wata matsala ta rayuwa da ake son nuna wa ga jama'a".

Kafin zuwan Turawa ƙasar Hausa, Hausawa suna da nau'o'n wasanninsu na gargajiya da suke aiwatarwa masu siffar kwaikwayo a dandali ko wajen bukukuwa da sauransu. Bayan zuwan Turawa ne Hausawa suka sami al'adar tsara wasan kwaikwayo a rubuce, ta haka ne aka samu rubutaccen wasan kwaikwayo na littafi irin su *Siɗ Hausa Plays* da *Wasan Marafa* da *Kulva Na Varna* da *Daƙiƙi Talatin*, da sauransu.

## 2.3.4 Adabi Na Rediyo

Adabin rediyo ba wani abu ba ne illa fasahar al`umma wadda a ka ƙirƙira da 'ka' aka wanzar ta hanyar na`urorin watsa sauti domin mutane su amfana. Fasahohin da ake wanzar wa a gidajen rediyo suna da yawa har ta kaima mutane suna yi wa kafar kirari da 'Dandamilin Makaho' wato mutum ko bashi da idon da zai ga wasannin kwaikwayon da ake gudanarwa a dandamali na musamman, ko kuma a talbijin, idan yana da rediyo zai iya saurara. A yayin da yake sauraro, yana iya gane duk wasu sautukan da aka yi amfani da su cikin wasan. Misali idan ana son a nuna ɗaya daga cikin ayyukan al` adar Bahaushe ta niƙa ko daka ko makamancin waɗannan sai kawai a yi amfani da sauti wajen bayyana aukuwar waɗannan abubuwa. Shi kuma mai saurare yana jin abubuwan da ake fadî zuciyarsa tana bashi hoton abin da ke faruwa.

## 2.3.5 Adabi Na Talbijin

Ma`anar adabin talbijin a nan ya ƙunshi hikomomi da fasahar al`umma waɗanda aka ƙirƙira da 'ka' aka kuma wanzar da su ta hanyar talbijin. Hikokmomin al`umma waɗanda ake tsara wa a ɗauka a na`urar ɗaukar ho to, kana a tace domin a yaɗa su ga jama`a suna da yawa. Kamar yadda ake wanzar da was an kwaikwayo a dandamali haka ake wanzar das hi a talbijin. Haka nan kuma akwai shirye-shirye waɗanda suka haɗa da wasa wassannin yara da gidan kasha ahu da wasannin kwaikwayo da waƙoƙin makaɗa iri-iri du kana ɗauka sa`annan a nuna su a talbijin. Saboda haka hanyoyin samar da adabin talbijin sun haɗa da ƙirƙira da baddalawa. Wasu shirye-shiryen sai an samar das u a wani nau`in adabin misali rubutacce ko na rediyo ko kuma na gargajiya kafin a sauya masa kamannu a kuma wanzar das hi ta kafar talbijin. Waɗannan ayyukan adabin su ake wa laƙabi da adabin talbijin.

### 2.3.6 Adabi Na Yanar Gizo

Yanar gizo ci gaban na`u`rorin sadarwa ya samar da ita, don haka ire-ire ayyukan da suke a talbijin ko rediyo ko makamancin waɗannan irin su fina-finai duk ci gaban fasaha ce ta ƙere-ƙere. Yadda ake tsara fasahar yanar gizo da adana su da kuma watsa su ga al`umma duk kusan iri ɗaya ne. Saboda haka a lura da cewa duk waƙoƙin fasihai ko kaɗe-kaɗe ko wasannin kwaikwayon da aka gabatar a talbijin ko rediyo ana iya gabatar da su ta yanar gizo. Wannan dalili ne ya sa wasu ke ganin akwai adabi musamman na yanar gizo.

Auna Fahimta

1. Kawo rabe-raben adabin zamani
2. Bayyana ma'anar rubutacciyar waƙa



## 2.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an tattauna ire-iren adabin zamani waɗanda suka haɗa da rubutacciyar waƙa da rubutaccen zube da rubutaccen wasan kwaikwayo da adabi na rediyo da na talabijin da kuma na yanar gizo

## 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Rubutaccen zube : - nau'i ne na zube da ake tsarawa, a wanzar a kuma adana a rubuce

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Kawo rabe-raben adabin zamani
i- Rubutacciyar waƙa
ii- Rubutaccen zube
iii- Rubutaccen wasan kwaikwayo
iv- Adabi na rediyo
v- adabi na talabijin
vi- adabi na yanar gizo

2- Bayyana ma’anar rubutacciyar waƙa
Rubutacciyar waƙa wani saƙo ne da ake gina shi a kan tsararriyar ƙa’ida ta baiti da ɗango da kari da amsa-amo da sauran ƙa’idojin da suka danganci daidaita kalmomi, da zavar su, tare da yin amfani da su, a rubuce sannan a rera lokacin da ake buƙata.

## KASHI NA UKU RUBUTATTUN WAƘOƘI

### bubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Ma’anar rubutacciyar waƙa
3.3.1 Tarihin Faruwar Rubutattun Waƙoƙi
3.3.2 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Ajami
3.3.3 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Boko
3.3.4 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Fina-Finai
Auna Fahimta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 3.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin za a kawo bayani ne kan rubutacciyar waƙa da ma’anarta. Sannan za a kawo tarihin samuwar rubutattun waƙoƙi cikin ajami da boko a taƙaice. Daga bisani kuma a kawo bayanin samuwar su cikin fina-finai.



### 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- ma’anar Rubutacciyar waƙa
- tarihin faruwarta tun daga ajami har zuwa boko
- yadda rubutun waƙar ya gangaro har zuwa fina-finai.



### 3.3 Rubutacciyar Waƙa

### 3.3.1 Ma’anar Rubutacciyar Waƙa

Masana da manazarta waƙoƙin Hausa sun yi musayar ra’ayi dangane da ma’anar waƙa, ta hanyar duba ga abin da waƙa ta ƙunsa, da kuma halayyarta.

A ganin Dangambo (2007) cewa ya yi:
*"Waƙa wani saƙo ne da aka gina shi kan tsarariyar ƙa'ida ta baiti, ɗango, rerawa, kari (bahari), amsa-amo (ƙafiya) da sauran ƙa'idojin da suka shafi daidaita kalmomi, zaben su da amfani da su cikin sigogin da ba lallai ne haka suke a maganar baka ba."*

A wani wurin kuma ya bayyana waƙa da cewa:
*"Waƙa wani furuci ne wato lafazi ko saƙo cikin azanci da ake aiwatawa ta hanyar rerawa da daidaita kalmomi cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da dabaru ko salon armashi."*

Shi kuwa Yahaya (2001) ya bayyana waƙa da cewa:
*"Waƙa tsararriyar Maganar hakima ce da ta ƙumshi saƙo cikin zavabbun kalmomin da aka auna domin maganar ta reru ba faɗuwa kurum ba."*
Ke nan idan aka dubi ma'anonin waƙa da aka kawo za a ga cewa, waƙa ta ƙumshi zaven kalmomi, da tsara su da daidaita su ta hanyar amfani da hikima domin isar da saƙo ga masu sauraro ko karanta ta.

### 3.3.2 Tarihin Faruwar Rubutattun Waƙoƙi

Kamar yadda masana suka nuna hanya ta farko da aka samu karatu da rubutu a ƙasar Hausa ita ce ta hanyar shigowar Musulunci. Masana tarihi sun nuna cewa Musulunci ya shigo ƙasar Hausa tun zamani mai tsawo.

Sarrafawar da Hausawa suka yi wa haruffan Larabci ta hanyar kwaskwarima da ƙago haruffan Hausa a ajamance, waɗanda babu su a Larabci misali. /v/, /ƙy/,/ƙw/,/ts/,/'y/ da sauran su, shi ya haifar da rubutun ajamin Hausa. Rubutu ya kankama, musamman daga ƙarni na 17 zuwa na 19, domin an sami bunƙasar ayyukan addini a rubutun ajami ta hanyar fassara littattafai da sauran ayyukan addini da kuma rubuta waƙoƙin addinin cikin ajami domin fadakarwa da ilmantarwa.

### 3.3.3 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Ajami

Ajami na nufin rubutun harshen Hausa cikin haruffan Larabci. Rubutun Ajami wani salon Rubutu ne da Bahaushe ya samar daga harufan Larabci. Wannan salon rubutu daɗaɗɗiyar hanya ce da aka yi amfani da ita a ƙasar Hausa. Hasashen binciko lokacin da aka fara rubuta waƙa da Hausar ajami ya nuna cewa a wajajen ƙarni na 17 ne aka fara. Masana sun kafa hujjarsu ne da cewa akwai wasu waƙoƙi na Hausa wadanda suka bayyana tun kafin haifuwar su Mujaddadi Shehu Usmanu. A littafin Yahaya (1988) ya yi bayanin cewa ana tsammanin akwai dadaddun waƙoƙi wadanda aka rubuta da Hausar ajami misali 'Shi'ir Hausa' da 'Wakar Jamuyah' na Sheikh Ahmad Tila da 'Tarikh El-Sudan' wadda Sheikh Abdulkadir Tafa ya rubuta da Hausa, amma sunan

wakar ya sa da Larabci. Haka nan akwai waka mai suna 'Shi'ir Hausa' ta Abdurrahman Tajuddin da mai suna 'Sartse' ta Mallam Alin Abubakar bin Kutunkura da kuma wasu waƙoƙi guda uku wadanda aka sa musu suna 'Wakar Hausa' amma ba a rubuta wanda ya yi su ba. A ƙarni na 17/18 akwai waka daya ta Wali dan Masani wadda ya rubuta mai suna 'Waƙar yaƙin Badar'. Wannan waka ta yabon Annabi (SAW) ce da kuma bayanin yadda Yakin Badar ya kasance. Bayan wannan waka an ci gaba da samun wasu waƙoƙi a ƙarni na 18 wadanda jigonsu suka ginu a kan addinin Musulunci. Akwai wani babban malami Malam Shi'itu dan Abdurra'uf wanda ya rubuta waƙoƙi cikin Larabci da Hausa. Cikin waƙoƙinsa na Hausa akwai 'Jiddul Ajizi' Ba'ajamiya, an kira ta Ba'ajamiya saboda fassarar 'Jiddul Ajizi' ce wadda ya rubuta da Larabci. Ita wannan waka littafin Mukhtasar ne, mawakin ya fassara a wake da Larabci da Hausa. Malam Shi'itu Dan Abdurra'uf ya ci gaba da rubuta waƙoƙi wadanda jigonsu duka na addini ne, kamar 'Wakar Tuba' (Jimiya) saboda wakar na karewa da harafin Ja, da 'Wawiya' wadda harafinta ke karewa da harafin Wa. A ƙarni na 19 ne aka sami ilmi ya kara zurfafa, karatu da rubutu suka kara bunƙasa, ayyukan addini suka ci gaba da wanzuwa, rubutu da ajami ya kara bunƙasa. Duk wannan ya faru ne saboda vullowar Mujadaddi Shehu Usmanu Danfodiyo a ƙasar Hausa. Shehu ya yi karatu mai zurfi, kuma saboda ilminsa da tsoron Allah da buri na gyaran al'umma sai Allah ya ba shi daukaka ya kuma cika masa wannan buri na gyaran al'umma ta hanyar ilmantarwa da wa'azantar da jama'a da yakin duk wata hanya ta alfasha da yin fito-na-fito da sarakunan Hausa masu zalunci a kan talakawa. Shehu ya tarar da al'ummar da ke cike da ayyukan masha'a da sharholiya, don haka ya tashi tsaye don kawo adalci da kawar da varna. Ta haka ne da shi da iyalansa da mabiyansa suka yi jihadi, suka kafa Daular Musulunci, suka kafa al'umma ta jama'a masu bin gaskiya da tsarin Musulunci.

Wannan yunkuri da suka yi ba zai dore ba sai da samuwar ayyuka na ilmi, saboda haka Shehu Usmanu da kanensa Abdullahi Fodiyo da 'ya'yansa Muhammadu Bello da Isan Kware da Abubakar Atiku da Nana Asma'u da sauran su, suka tashi tsaye domin yin rubuce – rubuce na fadakarwa. Haka nan sauran malaman jihadi suka bi wannan hanya don karantar da al'ummarsu.

Malaman jihadi sun yi namijin ƙoƙari wajen yin rubuce – rubuce da suka shafi fannonin addini kamar Tauhidi da Fiƙihu da Tarihi da siyasar Musulunci da sauran su. An yi bayanin cewa Shehu Usmanu shi kadai ya wallafa waƙoƙi fiye da ɗari huɗu da tamanin a cikin harshen Larabci da Fillanci da Hausa. Haka nan sauran malamai na wannan ƙarni sun duƙufa, kuma sun yi amfani da rubutacciyar waƙa wajen watsa addinin Musulunci da kau da zaluncin sarakuna da shugabanni da horo da alheri da hani da mugun aiki da ilmantarwa. Ke nan a wannan ƙarni ne aka fi samun bunƙasar rubutattun waƙoƙi a kan yabon Ubangiji da madahu da

fiƙihu da wa'azi da sauran fannoni na rayuwa. Masu jihadi sun wallafa waƙoƙi a kan addini domin kauce wa waƙoƙin hululu. Shehu Usmanu da `maƙarrabansa sun yi rubutun waƙoƙi da dama, misali Shehu ya rubuta waƙar "Ma'ama'are" da "Tabban Hakikan". Malam Abdullahi kuwa ya yi waƙar "Murnar cin Birnin Alkalawa" da waƙar "Tsarin Mulki na Musulunci". Sun ci gaba da rubuta waƙoƙin ilmantar da jama'a a kan ma'amala da rayuwar Musulunci da mulki da kasuwanci, misali, waƙar "Alhakin Mumuni Bisa Mumini" ta Isan Kware da wakar "Gargadi Ga Masu Shan Azumi" ta Nana Asma'u, (Sa'id, 1978). Bayan su Shehu sun yi aiki tukuru sun sami gyara al'umma, daga baya kuma sai shagala ta fara kunno kai, bidi'o'i suka fara yaduwa; sai malamai suka sake tashi tsaye don fadakar da tunatar da jama'a ta hanyar rubuta waƙoƙi, misali Waziri Buhari wanda ya rubuta waka a kan "Juye – juyen Zamani" da wakar "Shirin Guzuri Don Karatowar Mutuwa".

A takaice za a iya cewa a ƙarni na 19 ne aka sami habaka da bunƙasar rubutacciyar wakar Hausa, ba wani abu ya sa haka ba sai don saboda zaman ta mafi sauki wajen isar da sakon addini da ilmantar da jama'a. A littafin, ya yi bayanin cewa masu jihadi sun yi rubuce - rubucen waƙoƙi a kan jigogi 10, wato Tauhidi da Sira da Furu'a da Madahu da Nujumu da Hisabi da Wa'azi da Alhini da Tawassuli da Ilmantarwa. Kusan dukkan wadannan waƙoƙi suna da mabudi da marufi, wato farawa da rufewa da ambaton Allah da salatin Annabi. Haka nan tsarinsu na amsa-amo da ma'auninsu duk irin na waƙoƙin Larabci ne.

### 3.3.4 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Boko

Rubutun boko wani hanyar rubutu ne da Turawa suka zo da shi, wanda ake amfani da harufan Latinanci watau na Romawa wajen sarrafa su a rubuce domin karantawa.

Ƙarni na 20, ƙarni ne da Turawan Ingila, 'yan mulkin mallaka suka shigo Arewacin Nijeriya. A farkon ƙarnin ne, suka ci wannan yanki da yaƙi suka rusa daular Musulunci suka kafa makarantu domin koyar da ilmin boko wato maimakon amfani da haruffan Larabci wajen rubuta ajamin Hausa, sai suka kawo amfani da harufan Latinanci watau na Romawa wajen karatu da rubutu. Haka nan zuwan Turawa ya kawo sauye – sauye ga rayuwar Hausawa ta fannin tsarin mulki da ilmi da al'ada da siyasa da kere - kere da sauransu.

Tun da al'amarin tsarin mulki da ilmi ya koma hannun Turawan mulkin mallaka sai suka dukufa wajen samar da littattafan da za a yi amfani da su wajen koyarwa a makarantun boko, suka kuma fara rubuce – rubucen adabin Hausa, misali. J.F Schon ya rubuta littafin *Magana Hausa* da *African Proverbs* da sauran su; C.H. Robinson kuwa ya rubuta littafin

*Specimens of Hausa Literature*; Frank Edgar ya rubuta nasa littafi na *Tatsuniyoyi na Hausa.*

sTurawa sun ci gaba da ƙoƙarin bunƙasa karatun boko ta hanyar buɗe makarantu a manyan garuruwa kamar Kano da Sakkwato da Katsina, kuma harshen sadarwa shi ne harshen Hausa. Da abu ya yi nisa ne aka kafa Hukumar Fassara da Talifi da Kamfanin Norla da Hukumar Gaskiya da sauran su domin samar da ayyuka na ilmi. Waɗannan sauye–sauyen da aka samu a ƙarni na ashirin sun kawo sauye–sauye a fannin rubutun waƙa. A ƙarni na sha tara yawancin waƙoƙin Hausa da aka rubuta jigoginsu na addini ne, haka nan tsarin rubuta su, amma a ƙarni na ashirin da kida ya sauya sai rawa ma ta sauya, domin duk da cewa an ci gaba da taka tsohuwar rawa, wato rubutun waƙoƙi a kan addini, sai sabon salo ya bayyana na rubuta waƙoƙi waɗanda ba na addini ba. Haka nan marubuta waƙa sai suka fara gamin - gambiza, su ɗau tsarin addini a wani vangare su kawo wanda ba na addini ba a wani vangare. Cikin marubutan da suka fara bude kofa game da wannan salo akwai Sarkin Zazzau Aliyu dan Sidi, domin duk da yake waƙoƙinsa sun kasance na wa'azi da gargaɗi da ilimi, amma ya kawo wani salo wanda ya saba wa salon waƙoƙin ƙarni na sha tara.

Sarkin Zazzau Aliyu dan Sidi ya rubuta wata waka mai suna "Waƙar zuwa Birnin Kano", a inda ya yi bayanin ƙasaitaccen taron da aka yi a wannan gari.

A ƙarni na ashirin marubuta sun ci gaba da rubuta waƙoƙi a kan jigogi na addini, akwai irin su Aliyu Namangi da Nasiru Kabara da Akilu Aliyu da sauran su. Duk da an ci gaba da wallafa waƙoƙi cikin Hausar ajami, masu ilmin boko suna rubuta waƙoƙinsu da Hausar boko kuma suna rubutu a kan jigogin addini da sauran al'amura. An yi rubutu a kan neman ilmin boko da siyasar zamani da soyayya da kiwon lafiya da harkokin noma da na tattalin arziki da sauran su. Ke nan, za a iya cewa a wannan ƙarni na ashirin aka sami 'yan boko masu kishin addininsu da ƙasarsu da al'adarsu, suka tashi tsaye wajen faɗakar da al'umma ta hanyar rubuta waƙoƙi, cikin su akwai Mu'azu Hadeja da kuma wasu irin su Sa'adu Zungur, wanda ya rubuta waƙar 'Arewa Jumhuriya ko Mulukiya' da Aƙilu Aliyu da ya rubuta 'Hausa mai ban haushi' da Gambo Hawaja mai waƙar, 'A yau ba maƙi NEPU sai wawa'. Sai kuma Na'ibi Sulaiman Wali mai waƙar, 'Damina' da Hauwa Gwaram wadda ta rubuta waƙar, 'Ta'aziyar Sardauna' da sauran mawaƙa waɗanda suka rubuta waƙoƙi a kan jigogi daban – daban.

### 3.3.5 Rubutattun Waƙoƙi Cikin Fina-Finai

Waƙoƙin fina-finai, waƙoƙi ne da masu shirya fim suke tsara su kuma tsarma su a cikin fim domin su ƙayatar. Wasu manazartar sun ɗauke su a matsayin rukunin waƙoƙi baka na Hausa, dalilan kuwa su ne, saboda waƙoƙin suna tafiya tare da kiɗa da rawa da amshi da karveveniya. Ga kuma rashin tsarin baiti da rashin amsa amo da rashin ramzi da rashin mabiɗi da marufi. Tsarin waɗannan waƙoƙi iri guda ne da waɗanda aka sani na siyasa ko na dandamali/samartaka ko na buki ko na bege ko na talla da ake samu a wannan ƙarnin.

Masu ɗaukar waƙoƙin fina-finai a matsayin wani vangare na rubutattun waƙoƙin Hausa na zamani suna dogara da wasu dalilai kamar haka: Ana samun wasu waƙoƙin da tsarin baitoci duk da yake sukan sava a wasu baitocin, haka nan kuma sukan zo da amsa amo duk da yake a wasu lokutan yakan karye, akwai kuma samun marufin waƙa ko da kuwa babu mabuɗin waƙa.,

Auna Fahimta

1- Me ake nufi da waƙa rubutacciya?
2-Mene ne ajami? Kawo sunayen waƙoƙi biyar da aka rubuta cikin ajami da waɗanda suka rubuta su.

### 3.4 Taƙaitawa

A cikin wannan kasha an kawo bayani kan rubutacciyar waƙa da ma’anarta. Sannan an kawo tarihin samuwarta tun daga ajami har zuwa boko, daga bisani kuma aka kawo bayanin waƙoƙin fina-finai.

### 3.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

Waƙoƙin fina-finai:- waƙoƙi ne da masu shirya fim suke tsara su kuma tsarma su a cikin fim domin su ƙayatar.

## 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Me ake nufi da waƙa rubutacciya?

2- Mene ne ajami? Kawo sunayen waƙoƙi huɗu da aka rubuta cikin ajami da waɗanda suka rubuta su.

- Ajami na nufin rubutun harshen Hausa cikin haruffan Larabci. Rubutun Ajami wani salon Rubutu ne da Bahaushe ya samar daga harufan Larabci. Wannan salon rubutu daɗaɗɗiyar hanya ce da aka yi amfani da ita a ƙasar Hausa.
- Malam Shi'itu Dan Abdurra'uf ya yi wakar Tuba' (Jimiya)
- Mujadaddi Shehu Usmanu Danfodiyo ya yi waƙar "Ma'ama'are"
- Mujadaddi Shehu Usmanu Danfodiyo ya yi waƙar "Tabban Hakikan".
- Malam Abdullahi kuwa ya yi waƙar "Murnar cin Birnin Alkalawa"
- Malam Abdullahi waƙar "Tsarin Mulki na Musulunci".
- Isan Kware ya yi waƙar "Alhakin Mumuni Bisa Mumini"
- Isan Kware ya yi waƙar "Gargadi Ga Masu Shan Azumi"

## KASHI NA HUƊU RUBUTUN ZUBE

### Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Rubutun Zube
 4.3.1 Ma'anar Zube ta Zahiri
 4.3.2 Ma'anar Zube ta Lugga
 4.3.3 Ma'anar Zube Ilmi
4.4 Bambancin Zube da Waƙa
4.5 Bambancin Zube da Wasan Kwaikwayo
4.6 Samuwar Rubutun Zube a Ƙasar Hausa
 4.6.1 Zamanin Zuwan Musulunci
 4.6.2 Zamanin Zuwan Turawa
 Auna Fahimta
4.7 Taƙaitawa
4.8 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.8 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.10 Amsoshin Tambaypyin Auna Fahimta



### 4.1 Gabatarwa

Rubutun zube na Hausa al'amari ne da ya wanzu bayan samuwar karatu da rubutu a ƙasar Hausa. Saboda haka, rubutaccen zube na Hausa ya ratso zamunna mabambanta cikin tarihi. Wannan kashi ya ƙunshi bayanin ma'anar zube ta fuskoki uku wato ma'ana ta zahiri da ta lugga da kuma ma'ana ta ilimi, sai kuma bambancin zube da waƙa da wasan kwaikwayo. Sa'annan kuma akwai bayanin samuwar rubutaccen zube zamanin zuwan Larabawa da kuma zamanin zuwan Turawa.



### 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma'anar zube ta fuskoki uku, wato ta zahiri da ta lugga da kuma ta ilimi
- Mazaunin rubutaccen labari a adabin Hausa
- Bambancin rubutaccen zube da waƙa da wasan kwaikwayo
- Samuwar rubutaccen zube na Hausa a zangunna mabambanta tun daga zamanin
- zuwan Larabawa har zamanin zuwan Turawa.

## 4.3 Ma'anar Zube ta Zahiri

Zube kalma ce ta Hausa da ke da fuskoki guda biyu, da farko akwai fuskar lugga sa'annan akwai fuskar zahiri. A zahirance zube na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi, alal misali kara a zube, na nufin yadda karan ke warwatse ba tare da wani shiri ko tsari ba. Ke nan zube na iya nufin duk wani abu da aka yi shi ko aka tsara shi ba bisa bin wasu ƙa'idoji ko tsari ba.

### 4.3.1 Ma'anar Zube ta Lugga

Idan ana magana kan zube na lugga, yana nuna abin ya samo asali daga aikatau zuba, wato kamar ka zuba ruwa a kwano ko ƙasa, wannan shi ya haifar da kalmomi irin su zubar da ko zubewa ko zube ko kuma zubo daga cikin kalmomin aikatau na harshen Hausa, duk dai waɗannan na nufin abin da aka aikata na watsarwa ko yasarwa ko makamantan haka.

### 4.3.2 Ma'anar Zube Ilmi

Ida nana maganar ma'anar zube ta ilimi, to, ana batun ma'anar ne a fagen da ake nazari wato adabi. Saboda haka, a adabance zube na nufin guntattakan jawabai ko bayanai da ke zuwa kara-zube ba tare da wasu dokoki ko ƙa'idoji ba, sa'annan ana yin su ne domin a sa nishaɗi ko jin daɗi ga mutane. Ke nan zube na nufin abubuwa irin su tatsuniya da karin magana da tarihi da tarihihi da kirari da zambo da almara da ƙissa da ƙarangiya ko salon magana ko baƙar magana ko kuma rubutattun labarai (ƙagaggun labarai).

## 4.4 Bambancin Zube da Waƙa

Ɗangambo (1981) ya bayyana cewa; "waƙa wani furuci ne (lafazi ko salo) cikin azanci da ake aiwatarwa ta hanyar rerawa da daidaita kalmomi cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da dabaru ko salo mai armashi." Wannan ma'ana ta yi wa waƙa fyaɗar kaɗanya ne wato ta baka da kuma rubutacciya. Saboda haka, waƙa dai ƙirƙiren ƙwaƙwalwa ce, mai tsari na musamman, sannan kuma magana ce a dunƙule mai zurfi da kaifin ma'ana, (Yahya, 2012:230).

A nan ana iya bambanta zube da waƙa ta fuskar adabi, wato ana iya cewa a waƙa sai an tsara, an kuma shirya, sa'annan kuma a daidaita tunani kafin a aiwatar, alhali kuwa a zube ba a buƙatar waɗannan abubuwa. Ana ƙagawa ne sannan a gabatar kara-zube ba tare da takamammen tsari na baiti ko amsa-amo kamar waƙa ba.

## 4.5 Bambancin Zube da Wasan Kwaikwayo

Wasan kwaikwayo abu ne mai alamun wasa da kuma kwaikwayo. Shi dai wasa na nufin duk abin da ba gaskiya ba, yana kuma ɗauke da raha da ban dariya da nishaɗi, kwaikwayo kuwa na nufin aikata wanin abu don kwatanta yadda yake, ko yadda ake yin sa, ko don a nuna kyawunsa ko kuma muninsa.

A nan ana iya bambanta zube da wasan kwaiwayo ta fuskar adabi, wato ana iya cewa a sai an tsara, an kuma shirya, sa'annan a gabatar ta hanyar faɗi-in-faɗi(dialogue) da shigar burtu (wato kwaikwayo, alhali kuwa a zube ba a buƙatar waɗannan abubuwa. Ana ƙagawa ne sannan a gabatar kara-zube ba tare da bin tsari na faɗi-in-faɗi da shigar burtu kamar a wasan kwaikwayo ba.

## 4.5 Samuwar Rubutun Zube a Ƙasar Hausa

A kowace irin al'umma, ana soma rayuwa ne ba da hanyar rubutu ba haka nan kurum, ana soma gudanar da al'amurra ne da adabin gargajiya ko abin da wasu ke kira adabin baka, wanda ke gudana ne tattare da yadda al'amuran al'ummar ke wakana. Saboda haka, ana iya cewa tun farkon samuwar al'ummar ƙasar Hausa su ma ba da rubutu suka fara ba, da adabinsu na gargajiya ne suka wanzu. Kenan, ba wata hanyar rubutun zamani da Hausawa suka sani da ta wuce ta Larabci da Ajami ko kuma Boko. Samuwar wannan hanya ta rubutu, ita ta haifar da samuwar rubutaccen zube a ƙasar Hausa. Domin tabbatar da haka muka ga ya dace a bibiyi tarihi domin ganin yadda wannan batu ya wanzu.

### 4.5.1 Zamanin Zuwan Musulunci

Tun daga ƙarni na goma sha ɗaya (11) zuwa ƙarni na sha bakwai (17) tadojin Hausawa suka cuɗanya da aƙidojin Musulunci sakamakon shigowar Larabawa. Ta haka ne Hausawa suka fara fahimta da lizamtar halin rayuwa da al'adun Larabawa.

Hakan ya sanya suka naƙalci harshen Larabci da yadda ake rubuta shi. Wannan yunƙuri na ƙoƙarin iya karatu da rubutun Larabci da Hausawa suka himmatu a kai ya ba su damar ƙirƙiro wata hanyar rubutu ta kansu da sunan Ajami, wato rubutun Hausa, ta amfani da haruffan Larabci. Kodayake ba a sami daidaito dangane da lokacin da Hausawa suka fara rubutun Ajami ba, duk da haka an amince cewa rubutun Ajami ya daɗe a ƙasar Hausa, musamman tun a ƙarni na 14 da na15, (Malumfashi, 2009).

Samar da hanyar rubutun Ajami a ƙasar Hausa ya jawo rubuta adabin Hausa cikin yanayin zube. A ƙarni na goma sha bakwai (17), an sami rubuce-rubuce cikin ajami, kamar littattin ***Riwayar Annabi Musa,***

wanda Abdullahi Suka ya wallafa. Bugu da ƙari kuma an samar da waƙoƙi cikin Ajami gwargwadon hali. Haka aka ci gaba da samar tare da wanzar da rubutun Hausa, musamman na waƙoƙi, har zuwa ƙarni na goma sha takwas (18).

Daga wannan lokaci har zuwa ƙarni na goma sha tara (19), lokacin da Shehu Usmanu ya jaddada addinin Musulunci a ƙasar Hausa rubutun Larabci da Ajami ya sami ci gaba da inganta ta hanyoyi mabambanta, musamman ta fannin waƙoƙi da zube. Shugabannin jihadi irin su Shehu Usmanu Ɗanfodiyo da ɗansa Muhammadu Bello da ƙanensa Abdullahin Gwandu da 'yarsa Nana Asma'u da autansa Isan Kware da kuma wasu malamai da dama, sun agaza wajen rubuta waƙoƙin Hausa da kuma ayyukan zube. A wancan lokaci na su Shehu Usmanu, ba wai ana rubuta waƙoƙi ne cikin Ajamin Hausa kawai ba, a'a, har an mayar da wasu ayyukan zube na gargajiya cikin Ajami da kuma Larabci, (Malumfashi, 2009).

### 4.5.2 Zamanin Zuwan Turawa

Ko da Turawa suka shigo sassan ƙasar Hausa ba su shigo ƙasar a jahilce ba, domin suna da wata masaniya a kan mutanen wurin da kuma yanayin ƙasar. Tun kafin a kafa mulkin mallaka a ƙasar Hausa aka mayar da wasu sassan adabin bakan Hausa a rubuce cikin rubutun boko. Misalan waɗannan rubuce-rubuce sun ƙunshi tattara labarai da tatsuniyoyi da karin maganganu da sauran maganganun azanci da al'adun Hausawa wuri guda a takarda. Daga cikin littattafan da suka yi fice akwai ***Specimens of Hausa Literature*** na C.H. Robinson (1896) da kuma ***Hausa Stories and Riddles*** na H.C. Harris (1908) da ***Littafi na Tatsuniyoyi*** na Frank Edgar (1924) da ***Hausa Sayings and Folklore*** na Fletcher, R.S (1912) da sauran su.

Wannan tafarki da Turawa suka bi shi ne ya wanzar da abubuwan amfani dangane da rubutun bokon Hausa. Ta haka aka sami damar zama don kyautata nazari da kuma rarraba sigogin rubuce-rubucen zuwa azuzuwa mabambanta. Shi ya sa ko da Turawa suka mallake ƙasar Hausa, ayyukan adabi ta fannin tatsuniyoyi da labarai da maganganun azanci sun sami karɓuwa ta amfani da haruffan Romanci. Dangane da haka, zuwan Turawa ƙara taimakawa ya yi wajen kafa makarantun boko, inda ta haka ne aka daɗa faɗaɗa hanyoyin wanzar da rubutun Hausa.

Bayan kafa makarantun boko a ƙasar Hausa, Turawan mulkin mallaka sun kafa hukumomin inganta adabi domin samar da littattafan karantawa a makarantu. Tun kafin waɗannan hukumomi, **Hukumar ƙasa da ƙasa Ta Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka** ta shirya gasar rubuta labarai cikin harsunan Afirka a shekarar 1929. Labaran da suka sha yabo daga harshen Hausa sun kasance kamar haka; akwai H.B.G. Nuhu mai taken

***Hausa Stories*** da na Malam Dodo shi ma ***Hausa Stories***, sai na Malam Ahemet Metteden, mai suna ***Zaman Dara*** da na Malam Bello Kagara mai taken ***Littafin Karatu Na Hausa***, sai kuma na Malam Nagwamatse, mai suna ***Takobin Gaskiya***.

Hukumar farko ta inganta adabi da Turawan mulkin mallaka suka kafa a ƙasar Hausa ita ce **Hukumar Fassara** a shekarar 1929. Wannan hukuma ta samar da littattafai da suka haɗa da **Darussan Koyarwa Don Makarantun Elementare** da littafin ***Bayani Kan Cututtuka*** da kuma **Magaurayi**. A wannan shekara kuma aka kammala fassara littafin **Koyar Da *Kiwon Lafiya (II)***, aka kuma sake wa ***Aljaman Yara*** Rukuni, aka sake buga shi. Hukumar ta yi gyare-gyare ga littafin ***Labaru Na Da Da Na Yanzu***, inda aka fassaro sassan tarihin ƙasar Hausa da suke rubuce cikin harshen Larabci, aka zuba su a cikin wannan littafi.

Baya ga wannan ƙoƙari, har zuwa farkon shekarar 1933, hukumar fassara ta ga ba a sami littattafan adabin da take buƙata da suka shafi rubutaccen labarin Hausa ba. Sai hukumar ta shirya gasa ta biyu da ta taimaka wajen samar da littattafan adabin Hausa na farko ta fuskar zube daga 'yan gida. An dai shirya wannan gasa ne da manufofi biyu. Da farko a samar da ingantattun littattafan adabi, na biyu a sayar da littattafan, ba a raba kyauta ba kamar yadda aka saba yi a da. Wannan gasa ta samar da littattafai da suka inganta tare da kyautata adabin Hausa, an gudanar da ita ne a shekarar 1933. Ga sakamakon gasar kamar haka:

1. ***Ruwan Bagaja*** — Malam Abubakar Kagara (*An buga shi a* 1935)
2. ***Ganɗoki*** — Malam Bello Kagara (An buga shi a 1934)
3. ***Shaihu Umar*** — Malam Abubakar Bauchi (An buga shi a 1934)
4. ***Idon Matambayi*** — Malam Muhammadu Gwarzo (An buga shi a 1934)
5. ***Jiki Magayi*** — R.M East Da Tafida Umaru (An buga shi a 1934)

Duk da cewa waɗannan su ne aka zava a matsayin waɗanda suka ci gasar, akwai wasu da suka gamsar, aka tsara su don bugawa, amma ba a sami damar buga su ba, su ne:

1. ***Boka Buwaye*** na Malam Nagwamatse
2. ***Yarima Abba*** na Malam Jumare Zariya

Sai dai kafin wannan gasa ta 1933, W.R.S Miller da ƙungiyar Mishau ta C.M.S tuni suka fahimci amfanin wannan Rukuni na ƙaga labari, domin isar da saƙo, saboda haka sun fitar da littafin rubutaccen labari na farko da aka buga da harshen Hausa mai suna ***Fatima***, na Miller a 1933. Wanda da alama bai gamsar ba, shi ya sa ba a ji amonsa ba a cikin

karikitan rubutattun labaran Hausa tun wancan lokaci. Kila ba wani abu ya sa haka sai domin ba ya ɗauke da komi sai wa'azin Kirista da yaɗa manufofin addinin Kiristanci.

Baya ga hukumar Fassara, an cigaba da samar da wasu hukumomin da suka cigaba da bunƙasa samuwa da yawaitar rubutaccen zube na Hausa. Irin waɗannan hukumin sun haɗa da:

- Hukumar Fassara ta sauya suna zuwa Hukumar Talifi a shekarar 1936
- Kamfanin Gaskiya Da Jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo a shekarar 1939
- Hukumar NORLA a shekarar 1953
- Kamfanin NNPC a shekarar 1966

Tun daga wannan lokaci aka cigaba da samarwa tare da bunƙasa rubutaccen zube da samar da rubutaccen labarin Hausa, har zuwa shkekarun 1980 da al'amuran ɗab`i suka fara sauya Rukuni a arewacin Nijeriya, harkar samar da rubutaccen labarin Hausa suka fara ɗaukar wani sabon salo, samar da littattafan sai suka tashi daga kamfanonin na hukuma ko waɗanda hukumar ta amince da su, sai marubuta suka fara samar da littattafansu, suna fiddo su, sannan kuma Rukuni da jigon littattafan duk suka sauya daga yadda aka san su, suka koma na wasu jigogi daban. Wannan sabon Rukuni shi ne masana suka bayyana da Adabin Kasuwar Kano ko Labaran Soyayya da sauransu.

Auna Fahimta

1. Bayyana ma'anar zube ta waɗannan fuskoki;
   i. Ma'ana ta zahiri
   ii. Ma'ana ta lugga
   iii. Ma'ana ta ilimi/adabi

## 4.6 Taƙaitawa

Wannan gava ta ƙunshi bayanin rubutun zube, inda aka bayyana ma'anar zube ta fuskoki uku wato ma'ana ta zahiri da ma'ana ta lugga da kuma ma'ana ta ilimi, sai kuma bambancin zube da waƙa da wasan kwaikwayo. Sa'annan kuma an yi bayanin samuwar rubutaccen zube zamanin zuwan Larabawa da kuma zamanin zuwan Turawa.

## 4.7 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Zube: - na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi.

## 4.8 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Tsoho, M.Y. (1983). “Waƙeƙeniya”. Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Edward, B. T. (1967) “The Science of Culture” Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

4.9 **Amsoshin Tambaypyin Auna Fahimta**

1- Bayyana ma’anar zube ta waɗannan fuskoki;

i- Ma’ana ta Zahiri

ii- Ma’ana ta lugga

iii- Ma’ana ta ilimi/adabi

**Ma’anar Zube ta Zahiri**

Zube kalma ce ta Hausa da ke da fuskoki guda biyu, da farko akwai fuskar lugga sa’annan akwai fuskar zahiri. A zahirance zube na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi, alal misali kara a zube, na nufin yadda karan ke warwatse ba tare da wani shiri ko tsari ba. Ke nan zube na iya nufin duk wani abu da aka yi shi ko aka tsara shi ba bisa bin wasu ƙa’idoji ko tsari ba.

**Ma’anar Zube ta Lugga**

Idan ana magana kan zube na lugga, yana nuna abin ya samo asali daga aikatau zuba, wato kamar ka zuba ruwa a kwano ko ƙasa, wannan shi ya haifar da kalmomi irin su zubar da ko zubewa ko zube ko kuma zubo daga cikin kalmomin aikatau na harshen Hausa, duk dai waɗannan na nufin abin da aka aikata na watsarwa ko yasarwa ko makamantan haka.

**Ma’anar Zube Ilmi**

Ida nana maganar ma’anar zube ta ilimi, to, ana batun ma’anar ne a fagen da ake nazari wato adabi. Saboda haka, a adabance zube na nufin guntattakan jawabai ko bayanai da ke zuwa kara-zube ba tare da wasu dokoki ko ƙa’idoji ba, sa’annan ana yin su ne domin a sa nishaɗi ko jin daɗi ga mutane. Ke nan zube na nufin abubuwa irin su tatsuniya da karin magana da tarihi da tarihihi da kirari da zambo da almara da ƙissa da ƙarangiya ko salon magana ko baƙar magana ko kuma rubutattun labarai (ƙagaggun labarai).

# KASHI NA BIYAR RUBUTACCEN WASAN KWAIKWAYO, DA ADABIN REDIYO DA NA TALBIJIN

## Abubuwan da Suke Ciki

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufofin Darasi
5.3 Ma’anar Rubutaccen Wasan Kwaikwayo
5.3.1 Ire-Iren Wasan Kwaikwayo
5.3.2 Samuwar Rubutaccen Wasan Kwaikwayon Hausa
5.3.3 Wasan Kwaikwayon Farko-Farko
5.3.4 Wasan Kwaikwayon Tsakiya
5.3.5 Wasan Kwaikwayon Kwanan nan
5.4 Ma’anar Rediyo
5.4.1 Ire-Iren Adabin Rediyo
5.4.2 Tatsuniyoyi da Labarai
5.4.3 Wasa Ƙwaƙwalwa
5.4.4 Kacici-kacici
5.4.5 Wasan Kwaikwayo
5.5 Ma’anar Adabin Talbijin
5.5.1 Manufofin Gwamnati kan Wasannni
5.5.2 Ire-Iren Adabi Na Talbijin
5.5.3 Wasannin Kwaikwayon Talbijin
Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma’anar Wasu Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 5.1 Gabatarwa

A da can ba da nisa ba, idan ana maganar adabin Hausa da rassansa, ana ta ɗaukar rubutaccen wasan kwaikwayo a matsayin ɗan auta wanda ko lalle bai sha yadda ya kamata ba, bare ya samu tagomashin a-zo-a-gani. Amma binciken Ahmed, (1999-2012) ya tabbatar da ba shi ne ɗan autar ba. Samuwar wasannin kwaikwayo tun a 1898 ya nuna irin siraɗin da wasan kwaikwayo ya tsallake da ƙyar. Bayan nan kuma, marubucin wasan kwaikwayon da ya biyo baya shi ne Dr, R.M. East wanda ya rubuta littafin wasan kwaikwayo mai suna *“Siɗ Hausa Plays”*. Wannan marubucin ya gwada cewa ya yi wannan ƙoƙari ne don ya nuna wa Hausawa yadda za su iya mayar da tatsunniyoyinsu da labarai zuwa wasan kwaikwayo tare da fatar a iya, sa’annan a samar da waɗanda suka fi nashi kyau.

Dangane da adabin rediyo kuwa, sai mu ce muhimmancin wannan kafa ta rediyo wajen isar da saƙo ga al`umma ba ta misaltuwa, Ba kowa ne daga cikin al`umma suka mallaki talbijin ba, amma rediyo ganin sauƙin da yake da shi na mallaka sai ya kasance da wanda ke daji da wanda ke birni zai iya mallakar akwatin rediyo. Bare ma a wannan lokaci inda aka sauƙaƙa girmarsu da ingancinsu. Wannan dama ita tra sa mutane faɗin cewa rediyo ya fi kowace kafar sdarwa kusanci da al`umma. Saboda haka shirye-shiryen da ake yi ana gudanar das u domin su isa ga al`umma ne. Gwamnati ce ke da mallakar waɗannan gidajen rediyo, wasu daga cikin gidajen mallakar gamnatin tarayy ne, wasu kuwa na jihohi ne. A halin da ake ciki, an bayar da dammar samar da gidajen rediyo na `yan kasuwa, haka ta ƙara havakar samar da gidajen rediyo. Yawan su da kuma ƙirƙirar sababbin shirye-shirye waɗanda za su ka ga jama`a shi ya ɗaukar hankalin ma`aikatan waɗannan gidajen. Don haka a kulum rige-rige waɗannan gidajen suke yi wajen samar da shirye-shiryen da za su ƙayatar da jama`a.

Idan ana batun adabin talbijin kuwa, za a iya fahimtar cewa samuwar talbijin a Nijeriya ba wani abu ne mai daɗaɗɗen tarihi ba idan aka kwatanta da samuwar hanyoyin rubutu walau ta Ajami ko Boko. Abu ne sannane cewa sai da aka sami zaman dirshan na Turawan mulkin mallaka a ƙasar nan sa`annan aka sami wasu tsare-tsare na shugabanci da tattalin arziƙi da sauya akalar zamantakewar al`umma. Bayan wannan zaman dirshan na Turawa, sai `yan kishin ƙasa suka yi yunƙuri walau ta ɗabbaƙa wannan gini da Turawa suka yi ko kuma sauya su da waɗanda za su dace da tsarin zamantakewar al`umma. Akwai shirye-shirye masu tarin yawa da gidan talbijin yake da su.

## 5.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Ma`anar rubutaccen wasan kwaikwayo da yadda ya samu, ya kuma bunƙasa.
- Ma`ana da aikace-aikacen adabi na gidajen rediyo.
- Adabin rediyo da irin matsayin da yake da shi wajen ilmantarwa da faɗakarwa da kuma nishaɗantar da al`umma.
- Ma’anar adabin talbijin.
- Dalilan da karve gidajen talbijin na shiyyoyi da gwamnatin tarayya ta yi.
- Manufofin gwamnatin kan wasannin kwaikwayo

## 5.3 Ma'anar Rubutaccen Wasan Kwaikwayo

Masana da manazarta wannan fanni na wasan kwaikwayo sun taka muhimmiyar rawa wajen bayyana yadda yake da rabe-rabensa, Yahaya, (1978) da Ahmed, (1985) da Koforowola, (1978). Wasu sun yi nazarin asali da yadda rubutaccen wasan kwaikwayo ya bunƙasa, Malumfashi, (1985 da 1990). Yayin da wasu suka duba asali da bunƙasarsa, wasu kuwa sun duba gudummawa ko muhimmancinsa ko akasin haka da wasannin suke bayarwa ga al'ummar Hausawa, Malumfashi, I (1990). Akwai kuma da yawa daga cikin kundayen da aka rubuta na neman digiri tun daga mataki na farko har zuwa digirin digirgir kan muhimmaninsa da haɓakarsa ko nazartar wasu fannoni ko saƙonnin da wasannin suke ɗauke da su. Rubutaccen wasan kwaikwayo na nufi wasan da aka rubuta don a karanta, aka kuma gabatar da shi gaban masu kallo a dandamali.

### 5.3.1 Ire-Iren Wasan Kwaikwayo

Masana sun rarraba wasan kwaikwayon Hausa ta fuskoki da dama. A yayin da wasu suka yi rabon ta fuskar lokaci, watau gargajiya da na zamani. Wasu kuwa sun yi ne ta fuskar masu gudanar da ire-iren wasannin. Yahaya, (1978) ya raba wasan kwaikwayo gida huɗu kamar haka:

i. Wasannin Gargajiya irin na tashe misali Ga Mai Rama, da Karo ba Shawara.
ii. Aikataccen wasa irin wanda akan yi a dandamali da gidajen Talbijin don a yi kallo.
iii. Wasan kwaikwayo da ake yi a gidajen Rediyo don a saurara, amma ba a gani.
iv. Rubutaccen wasan kwaikwayo wanda yakan zo a tsarin littafi don a sami abin karantawa.

Shi kuwa Ahmed. (1985) ya rarraba wasan kwaikwayo ne kamar haka:

a. Wasannin Kowa da Kowa. Misali: Tashe, da Giwa sha laka, da Bukin cikan shekara, da Bukin buɗin daji.
b. Wasannin Matasa. Misali: Kalankuwa, da Wowwo, da Taƙai, da 'Yar tsana.
c. Wasannin Masu Sana'a. Misali: Bori, da 'Yan kamanci, da 'Yan hoto, da Wawan Sarki.
d. Wasannin Lalura. Misali. Roƙon ruwa, da husufi.
e. Wasannin Zamani. Misali: Rubutattun wasanni, da wasannin Rediyo, da wasannin Talbijin.

Wani rabon da aka yi kuma shi ne wanda ke nuni da karkasa wasan kwaikwayo ta kafofin isar da saƙo ko aiwatar da shi.

1). Rubutaccen Wasan Kwaikwayo: Wannan shi ne wanda ake rubutawa a littattafai don karantawa.
2). Wasan Kwaikwayo na Rediyo: Shi ne wanda ake watsawa a Rediyo don sauraro
3). Wasan Kwaikwayo na Dandamali: Wanda ake aiwatarwa a zahiri don a kalla kuma a ji.
4). Wasa Kwaikwayo na Talbijin: Wanda ake nunawa a Talbijin.
5). Wasan Kwaikwayo na Fim: Ya shigo daga baya ne, shi ne ake ɗauka a kaset da faifan CD, kuma a nuna a talbijin. Ɗangambo, (1984).

Wasu kuwa su yi rabon ne zuwa gida biyu, wato wasan kwaikwayo na gargajiya da wasan kwaikwayo na zamani, Sambo, (2012).

### 5.3.2 Samuwar Rubutaccen Wasan Kwaikwayon Hausa

Idan ana batun tarihin wasan kwaikwayo a kowace al'umma ya dace ne a koma ga al'adu da adabin gargajiya domin ganin ko akwai wasu wasanni masu kamannu da irin wannan abu. Idan aka nazarci al'adun Hausawa a taƙaice, za a iya cewa wasan kwaikwayo ya samo asali ne tun farkon ginuwar al'ummar Hausawa. Ita wannan al'umma tana tafiya ne da al'adunta na gargajiya da suka haɗa da wasannin gargajiya da sauran wasanni. Wasan kwaikwayo ya samu ne ga al'ummar Hausawa tun kafin wanzuwar ilmin zamani na karatu da rubutu. Da daɗewa akwai wasu al'adu da yara ko samari suke gabatarwa ta hanyar kwaikwayo a tsakaninsu shekaru aru-aru kafin al'ummar Hausawa su fara hulɗa da cuɗanya da wasu al'ummomi na ƙetare (Yahaya, 1978 da Kofoworola, 1978 da Ahmed, 1987).

Larabawa dai sun shigo ƙasar Hausa ta hanyoyi mabambanta, da farko dai a lokacin shigo da addinin Musulunci wanda aka ce ya sami karɓuwa tun wajajen ƙarni na 8 zuwa na 9, daga baya kuma ta hannun masu cinikin bayi da saye da sayarwa, addinin Musulunci ya zaunu sosai a ƙasar Hausa. Daga tsakanin ƙarni na 13 zuwa na 15 kuwa addinin Musulunci ya warwatsu zuwa garuruwa da ƙauyukan ƙasar Hausa, ta yadda kusan kowane sashe na ƙasar Hausa ana gudanar da addinin Musulunci. Wannan ya sanya ilmin addinin Musulunci da makarantun allo suka wanzu a kusan ko'ina a faɗin ƙasar Hausa. Wannan ne ya sa al'ummar yankin suka naƙalci harshen Larabci ta yadda har suka iya rubutu da shi, suka samar da hanyar rubutu ta ajami. Saboda haka har zuwa lokacin da aka yi jihadin addinin Musulunci a ƙasar Hausa a ƙarni na 19, wanda Shehu Usmanu [anfodiyo ya yi a 1804, za a ga cewa yawancin Hausawa sun iya karatu da rubutu cikin Larabci da ajami ta yadda aka samar da rubutaccen adabin Hausawa ta waɗannan hanyoyin

rubutu, yawancin ayyukan adabin da aka samar sun fi a fagen waƙa da kuma zube amma ban da wasan kwaikwayo. Haka nan lokacin da Turawa suka zo ƙasar Hausa sun yi ƙoƙarin mayar da wasu wasannin da tatsunniyoyi zuwa rubutaccen wasan kwaikwayo kamar yadda Dr. R. M. East ya tsara wasan kwaikwayo na Hausa a shekarar 1936, wanda aka sa wa suna *Sidꞌ Hausa Plays.* Wannan ne wasu ke ganin shi ne rubutaccen wasan kwaikwayo na farko a al'ummar Hausawa kafin a sami wasu su biyo baya.

Mai wannan ra`ayi Yahaya (1978:250), na ganin duk da hulɗar da aka yi da Larabawa, da kuma iya karatu da rubutu da harshen Larabci wanda ya kai ga ƙirƙirar Ajami, akwai wasu dalilai da suka hana samuwar wasan kwaikwayo da ajami. Waɗannan hujjoji da ke biye su ne masanin ya gabatar na dalilan da suka hana samuwar wasan kwaikwayo da rubutun Ajami.

a) Ajami ya zo ne da addini, saboda haka an fi yin amfani da shi wajen rubuta waƙoƙin wa`azi da bayanin fannonin addini.

b) Su kansu Larabawa waɗanda al`adunsu suke da babban tasiri kan Hausawa sai wajen ƙarni na18 suka fara rubuta littattafan wasannin kwaikwayo. Saboda haka suma bai gama ratsa su ba balle su ɗanɗanawa wasu.

c) Addinin Musulunci ya hana al'adu na wasannin banza da labaru na ƙarya da waƙe-waƙe na hululu. Saboda haka Malaman addini ba ruwansu da wasa balle har a ce su ƙarfafa shi ta rubutun wasan kwaikwayo.

d) Babu wani jadawali mai bayar da damar yin wasu abubuwa kamar wasanni daban.

Wasu kuwa irin su Ahmed, (1987) da Malumfashi, (1985 da 2014) gani suke waɗannan dalilan da aka gabatar na rashin samuwar wasan kwaikwayo ba su isa a ce babu shi gaba ɗaya ba. Samuwar wasu rubutattun wasan kwaikwayo wanda wani Bajamushe mai suna Dr Rudolf Prietze da shi da Ahmadu Kano suka rubuta har guda shida (daga labarin da Alhaji Ahmadu Kano ya ba Prietze) tun daga kan *Turbar ƙudus, (1898)* da *`yan Matan Gaya, (1900)* da *Tarihin Rabe, (1902)* da *Turbar Turabulus, (1902)* da *Wasan Gizo da ƙoƙi da wasan Boka da Majinyaci, (1910), Malumfashi,* (2013) sun tabbatar da cewa an sami rubutattun wasannin kwaikwayo da Ajami.

### 5.3.3 Wasan Kwaikwayon Farko-Farko

Rubutaccen wasan kwaikwayon da aka fara ɗauka a matsayin na farko shi ne wanda Dr R.M East da malam Abubakar Imam da masinjar hukumar malam Basankare suka tsara wasan kwaikwayo na farko da Hausa a shekarar 1936, wanda suka sa wa suna Siɗ Hausa Plays (Wasannin Hausa guda shida).

Daga cikin dalilan da ya sa aka soma wannan al'ada bai wuce neman nuna wa jama'a yadda ake tsara wasannin kwaikwayo a rubuce ba, musamman ta hanyar canza tatsuniyoyi da tarihi da tarihihin ƙasar Hausa zuwa wasannin kwaikwayo. Ganin wannan littafi ya amsu, yara kuma suna karantawa ga kuma lokutta da aka ajiye a azuzuwa domin yin wasannin da kuma shirya wasannin kwaikwayo, sai wannan al'ada ta shige rayuwar jama'a, daga wannan lokaci yara da malammai suka shiga rubuta da aiwatar wasannin kwaikwayo a makarantu da lokutan karatu da bukukuwa.

Daga cikin ɗaliban farko da suka rubuta wasannin kwaikwayo aka gabatar sun haɗa da irin su malam Aminu Kano, Alhaji Yusuf Maitama Sule, Alhaji Abubakar Dogondaji da Alhaji Abubakar Tunau Mafara, Wasu kamar na malam Aminu Kano Kai Wanene a Kasuwar Kano? Da Gudumar dukan en-en Kano, ba a buga su ba, sai littafin Alhaji Abubakar Tunau Mafara, Wasan Mafara (1949) da na Alhaji Abubakar Dogon Daji, malam Inkuntum, (1953), waɗanda aka buga daga baya.
Shi kuwa Malumfashi, (1990) na cewa:

Abin da nake gani a iya cewa a game da litattafan wasan kwaikwayo in har sai an ce wani abu shi ne sun fi bunƙasa a tsakanin 1970-1980. Daga 1930-1940 an sami guda ɗaya. Babu ko ɗaya daga 1940-1950. An haifi uku daga 1950-1960. Littafi ɗaya rak aka samu daga 1960-1970. Daga 1970-1980 ne aka samu kimanin guda tara. Sai kuma daga 1980-1990 wanda huɗu ake jin an samar. Malumfashi, (1990:42). Don haka wasannin Rudolf da R. M East da waɗanda su Alhaji Abubakar Tunau Marafa da Alhaji Abubakar Dogon Daji suka rubuta su ne wasannin kwaikwayon farko farko.

## 5.3.4 Wasan Kwaikwayon Tsakiya

Wasannin kwaikwayon tsakiya kuwa su ne waɗanda suka samu bayan bunƙasar tattalin arziƙin ƙasa, a wuraren 1970 zuwa 1980 aka sami wasannin kwaikwayo guda tara waɗanda suke bayyana halin rayuwar wannan lokaci. Bunƙasar tattalin arziƙi ya sa mutanen karkara barin ƙauyukansu suna kwarara ga birane da alƙaryu, wannan kwararar ta haifar da wasu sauye-sauye a tsarin zamantakewar al`umma wanda marubuta wasannin kwaikwayon suka yi amfani da wannan damar wajen rubuta littattafansu.

## 5.3.5 Wasan Kwaikwayon Kwanan nan

Wasannin kwanan na su ne waɗanda suka samu daga 1980 zuwa wannan lokaci da muke ciki. Su ma kamar sauran, suna bayyana yadda rayuwar al`umma ta kasance na wannan lokacin, A yanzu an sami ci gaban rayuwa da wayewar kai da neman `yanci da gwagwarmaya da ci

gaban ilmi. Inda ka sami waɗannan abubuwa dole ne adabinsu ta sauya wanda zai bayar da hoton tsari rayuwar al`ummar da ake ciki.

## 5.4 Ma'anar Rediyo

Wannan kalma dai asalinta Baturiya ce wato "Redio" wadda take nufin na'ura ta sadarwa ta hanyar iska ba tare da haɗe-haɗen waya ba. Ana amfani da rediyo ne don isar da saƙo ga jama'a ta fuskoki da dama. Kuma saƙon, murya kawai yake bukata yadda masu sauraro za su iya ji da kunnensu tamkar suna kallon mai magana.

Idan ana maganar rediyo, kamar yadda Malumfashi, A.I. (2011) ya bayyana, to dole ne a tuna da mutumin nan mai suna "Guglielmo Marconi" wanda aka nuna cewa gudummawarsa ce ta samar da wannan na'ura a fili. An ce imaninsa da ya yi cewa za a iya aikawa da saƙo ta sauti ne ya sa ya bar ƙasarsu ya koma Ingila a shekarar 1896 saboda ya lura ba ya samun goyon baya a ƙasarsa. Ko a Ingilan ma, da ya kafa kamfaninsa na sadarwa a shekarar 1897, wasu `yan kasuwar ƙasar Ingila, gani suke yi ya zautu. To amma aka ce duk da haka bai karaya ba, nacewarsa da ya yi ne ta haifar da abin da ake kira rediyo a yau.

Rediyo ba ƙashin yadawa ba ne saboda muhimmancin ga jama`a. Ba za a fahinci hakan ba, sai lokacin da mutum ke kallon talabijin ko majigi, kwatsam! Sai a ji murya ɗif, to nan da nan za ka ji an koka duk kuwa da cewa ga hoton ana gani. Sannan rediyo ita ta fi arha wajen isar da saƙo ba tare da wani shamaki ba, walau a Maraya ko a wajen marayu. A karkara, a gida ko a jeji ko a ruwa ko kan tsauni. Wannan ya ba jama'a damar mallakar ta don saurarон shirye shirye masu amfanar da su yau da kullum.

### 5.4.1 Ire-Iren Adabin Rediyo

Hikima da fasahar al`umma waɗanda aka tsara su a gidajen rediyo kuma aka gabatar das u ta wannan hanyar sadarwa su aka yi wa laƙabi da adabin gidan rediyo. Wasannin kwaikwayo da tatsuniyoyi da wasa ƙwaƙwalwa da labarai da kaɗe-kaɗe da ake shirya su a gidajen rediyo kaɗan ne daga cikin ɗinbin shrye-shryen ayyukan adabi na gidan rediyo. Ba ta yiwuwa a wannan ƙanƙanen lokaci a ce an fayyace kowani shiri na gidan rediyo a matsayinsa na adabi, duk da haka nazarta wasu daga ciki zai fayyace mana abin da ake nufi da adabin gidan rediyo.

### 5.4.2 Tatsuniyoyi da Labarai

Shirin tatsuniyoyi da labarai waɗanda ake gabatarwa a gidajen rediyo sun ƙunshi tsararrun labarai ne da tatsuniyoyi waɗanda mutane suka yi suka kuma aika da su gidajen rediyo domin a watsa wa al`umma. Za a

iya samun wasu daga ciki su kasance littattafan zube ne ko sanannun tatsuniyoyi waɗanda suke kai-komo a cikin al`ummar Hausawa sai wasu daga cikin masu sauraro su ɗauka su aika da su gidajen rediyo domin a rinƙa karantawa jama`a. Wasu kuwa ba a tava samar da su ta wata kafa ta sadarwa ko ta rubutu in ba an wannan lokaci ba. Waɗannan hanyoyi biyu na samar da tatsuniyoyi da labarai su ake son a fahoimce su da kyau, da farko dai idan an riga an samar da wannan aikin adabi ta wata kafa musali rubutacce ko ta talbijin ko dandamali, sa`annan daga baya aka wanzar da wannan aikin adabi ta kafar rediyo, to wannan aiki yana nan a matsayinsa na asali. Wato idan adabin rubutacce ne tun farko, yana nan a wannan matsayi. Idan kuwa aikin adabin ƙirƙirarsa aka yi aka kuma fara wanzar da shi ta kafar rediyo, ya zama adabin rediyo. In ma an sake wanzar da shi ta wata kafar sadarwa misali talbijin ko kuma an rubuta shi, shi ma matsayinsa na adabin rediyo bai sauya ba.

### 5.4.3 Wasa Ƙwaƙwalwa

Da jin sunan an san ya riga ya bayyana kansa. Shiri ne da za gabatar da wata matsala mai sarƙaƙiya wadda take neman zurfafa tunani kafin a warware matsalar da aka gabatar. Sau da yawa wasa ƙwaƙwalwa na buƙatar a natsu domin a ga yadda za a iya warware taƙaddamar da ke cikin labari ko bayani. Wani lokaci akan buƙaci ra`ayin mutuim ne ta hanyar tambaya, idan kai ne yaya za ka yi? Ko shakka babu hikimomin da sarrafa harshen da wannan vangare ya ƙunsa sun nuna yanayin ci gaban harshen Hausa da yadda al`umma ta ɗauki rayuwa. Tawaɗannan hanyoyi, ana ilmantar da al`umma haɗe da koyar dadabarun zaman rayuwa.

### 5.4.4 Kacici-kacici

Kacici-kacici hikima ce wadda ta ƙunshi ƙoƙarin gano wani abu ko kuma yadda abu zai kasance ko warware wata matsala. An fi yin kacici-kacici na gidan rediyo ga manyan mutane, inda za a a yi tambaya mutane su bugo waya domin bayar da amsa. Wani lokaci ma mutum da kansa zai zavi lambar tambayar da yake buƙata a karanta masa, wannan ba yaa nufin ba a yi wa yara ba. Kacici-kacici hikimace da ta ƙunshi sarrafa harshe. A wani lokacin ana siffanta wasu kalmomi da ma'anarsu, don a sa yaro ko banbba su yi ƙoƙarin gano ma`anonin kalmomin da kuma dangantasu.

### 5.4.5 Wasan Kwaikwayo

Ɗaya daga cikin vangarorin da wasan kwaikwayo ke samun gudunmawa mafificiya shi ne ta kafar sadarwa, musamman gidajen rediyo. Gidajen rediyo sun daɗe suna shirya wasannin kwaikwayo da nufin faɗakarwa da ilmantarwa da nishaɗantarwa da yin hannunka mai sanda ta fuskar

wayar da kan jama'a dangane da al'adunsu da kuma aikace-aikacen hukumomi. Gidan rediyo da talabijin na farko na Arewa shi ne RTK wanda aka kafa a shekara ta 1962. Gidan rediyo ne haɗe ta talbijin duk a lokci guda kuma shirye-shiryen an tsara su domin su kasance sun bayyana manufar gwamnati kan abubuwan da suka shafi ilmi da shugabanci da tattalin arziƙi da hadîn kan ƙasa. Daga baya ne aka rinƙa yin shirye-shirye waɗanda za su ƙayatar da alumma su, ta nan ne aka fara wasannnin kwaikwayo na rediyo. Babu wani tabbas na cewa ga ranar da aka fara wasan kwaikwayo na rediyo

Wasan kwaikwayo ya bunƙasa a sanadiyar ƙara jihohi don kuwa kusan a wannan lokaci kowace jiha na ƙoƙarin ta riƙa aiwatar da tata basirar. Tsafaffin wasannin kwaikwayo na farko-farko sun haɗa da Basafce Na Kumatu Mai Karen Kamun Kura da Zaman Duniya Iyawa ce da Gundumi Fasa Kwanya da Jami`ar Jatau Na Albarkawa.

Tun daga wancan lokaci ne aka ci gaba da samun wasannin kwaikwayo a kafafen rediyo har ma da talabijin, inda shahararren 'yan wasa irin su Alhaji Yusuf Ladan da Alhaji Shu'aibu Maƙarfi suka riƙa bayar da gudunmawa ga tsarawa da rubuta wasannin kwaikwayo kuma aka riƙa yin su a rediyon Jihar Kaduna. A cikin shekarun 1970 aka sami wani tsohon saja wato Usman Baba Fategi (Samanja) ya vullo. Haka dai abubuwa suka yi ta ci gaba har Hukumomin Talabijin da Rediyo na wasu Jihohi, kamar Kano da Filato (Jos) da makamantansu suka riƙa aiwatar da wasannin kwaikwayon Hausa. (Sun Ɗiaomeng, 2013: 85).

A yau, gidajen rediyo manya da ƙanana, na Gwamnati da masu zaman kansu suna shirya wasannin kwaikwayo da dama domin ilmantarwa da faɗakarwa da kuma nishaɗantar da al'umma.

## 5.5 Ma'anar Adabin Talbijin

Ma`anar adabin talbijin a nan ya ƙunshi hikomomi da fasahar al`umma waɗanda aka ƙirƙirƙa da ka aka kuma wanzar da su ta hanyar talbijin. Kafin mu yi nisa ya kamata a san manufofin Gwamnatin Tarayya game da Shirye-shiryen Talabijin, a shekara ta 1975 lokacin da aka ƙara yawan Jihohin ƙasar nan zuwa goma sha tara gwamnatin tarayya ta karaya da cewa yawan gidajen Talabijin na iya ƙaruwa, kuma cin gashin kan da suke da su da kuma alamomi na rarrabuwar kawuna kan kishi na yankuna na iya ƙaruwa, sai gwamnatin tarayya ta yanke shawarar karɓa da mallakar duk wasu gidajen Talabijin a wannan lokaci.

Dokar soja mai lamba 24 ta 1977 wadda ta fara aiki tun ɗaya ga watan Afirilu 1976 ta mallaka duk wani gidan talabijin a ƙarƙashin majalisar mulkin soja ta ƙasa. Wannan doka ita ta kafa gidan Talabijin mallakar gwamnatin Tarayya mai suna (Nigerian Television Authority 'N.T.A.').

An ba ta alhakin yaɗa shirye-shirye ba tare da nuna bambancin son kai ko yankuna ba.

Egbon, (1982:27) ya bayyana dalilan da gwamnatin tarayya ta bayar wajen karɓe waɗannan gidajen Talabijin kamar haka:

a. Ta aikata ko cika duk wani abu wanda ya shafi ƙasa baki ɗaya, ba kawai abubuwan siyasa ko wani ɓangare na ƙasa ba.
b. Don ta nuna ƙarara a kan gudanarwa da manufofi masu yawa da bambancin al'umma da ƙasa ta ke da shi, duk da wannan bambance –bambancen ƙasa na da haɗin kai.
c. Don 'yan ƙasa su amfana da kyawawan al'adun da ke ko' ina a cikin ƙasar ta hanyar nuna su a gargajiyance.
d. Don taimakawa wajen ilmantarwa da nishaɗantarwa da ƙarin ƙarfin guiwar al'ummar ƙasa.
e. Don samar da al'adu da wasu shirye – shiryen da za a iya tallatarwa ga ƙashashen waje.

Waɗannan su ne dalilan da gwamnatin tarayya ta bayar wajen jaddada karɓe waɗannan gidajen ya zama mallakin gwamnatin tarayya. Har zuwa shekara ta 1979 akwai gidajen talabijin na ƙasa guda ashirin da ɗaya a duk manyan biranen jahohin da ke ƙasar nan da kuma guda ɗaya da aka aza tubalin gini a Abuja.

Uzodima, (1981sh. 9) ya nuna cewa daga wannan lokaci ne N.T.A. ta raba ƙasar zuwa yankuna shida ta yin la'akari da al'adu da kusantar waɗannan wurare. Ta karkasa gidajen talabijin a ƙarƙashin yanki – yanki. Kowane yanki yana ɗauke da Jihohi uku in ban da yankin B wanda yake ɗauke da Jihohi huɗu. Yankunan su ne kamar haka: -

a. N.T.A Abekuta da Ikeja da Ibadan, Ibadan ce cibiya.
b. N.T.A Aba/Owerri da Akure da Portharcourt da Benin, Benin ce cibiya.
c. N.T.A. Calabar da Makurdi da Enugu, Enugu ce cibiya.
d. N.T.A. Jos da Kano da Kaduna, Kaduna ce cibiya.
e. NTA Bauchi da Yola da Maiduguri, Maiduguri ce cibiya.
f. N.T.A. Ilorin da Minna da Sokoto, Sokoto ce cibiya.

Waɗannan manufofi na karɓe waɗannan gidajen yaɗa labarai na ƙara tabbatar da wannan ra'i mai nuna cewa gwamnati na tsare-tsare domin ganin ta daidaita tunanin al'umma da haɗin kan 'yan ƙasa.

### 5.5.1 Manufofin Gwamnati kan Wasannni

Idan kuwa ana batun manufofin gwamnati kan wasanni ko kuma mu ce wasannin kwaikwayo na talabijin, nan ma akwai bayanai ƙarara waɗanda suka kasance fitila mai haskaka ire-iren wasannin da za a

samar. Hukumar gidan talabijin ta ƙasa ta bayyana ƙarara manufofin gwamnati kan ire-iren wasan kwaikwayon da take buƙata kamar haka :

- Domin Ilmantarwa da faɗakarwa da nishaɗantarwa.
- Tallatar da kyawawan al'adu da ɗabi'un al'umma.
- Don haɓaka da ƙarfafa fasahar wasanni da kuma wasannin kwaikwayo rubutacce da aiwatacce (dandamali da talabijin).
- Don Fito da munanann ɗabi'u da hanyoyin magance su.
- Don bayyana hoton rayuwar al'umma.
- Don ƙarfafa kyawawan tunani da kishin ƙasa.
- Don a faɗakar da al'umma kan su rungumi kyawawan tunani.

Ko da yake wasu na ganin wannan a matsayi tarnaƙi domin kuwa ba a sake wa gidajen talabijin akala wajen aiwatar da duk wasu wasannin kwaikwayon da suka ga dama ba, wannan tarnaƙi na daga cikin matsalolin da suka addabi gidajen talabijin wajen samar da wasan kwaikwayon Hausa.

### 5.5.2 Ire-Iren Adabi Na Talbijin

Kamar yadda bayani ya gabata kan rediyo hikimomi da fasahhohin al`umma waɗanda aka tsara su a gidajen talbijin kuma aka gabatar da su ta wannan hanyar kafar sadarwa su aka yi wa laƙabi da adabin gidan talbijin. Wasannin kwaikwayo da tatsuniyoyi da wasa ƙwaƙwalwa da labarai da kaɗe-kaɗe da ake shirya su a gidajen talbijin kaɗan ne daga cikin ɗinbin ayyukan adabi na gidan talbijin. Shirye-shirye irin su gidan kashe ahu da Ba ta yiwuwa a wannan ƙanƙanen lokaci a ce an fayyace kowani shiri na gidan rediyo a matsayinsa na adabi, duk da haka nazarta wasu daga ciki zai fayyace mana abin da ake nufi da adabin gidan rediyo.

### 5.5.3 Wasannin Kwaikwayon Talbijin

Shigowar Talabijin a Nijeriya ya wanzar da samuwarsa ne kawai a birane da alƙaryu babu a ƙauyuka da karkara inda mafi yawan talakawa suke zaune. Daɗin daɗawa kuma a ƙauyukan da karkara babu wutar lantarki da za a yi amfani da waɗannan akwatunan Talabijin ɗin. [an karar tsadarsu, su kansu akwatunan Talabijin ya sa talakawa ba sa iya sayansu. Mahukunta a wannan lokaci suna amfani da gidajen talabijin ne wajen yayata manufofi na gwamnati. Daga baya suka fahimci cewa akwai buƙatuwar a kawo wasu shirye-shirye waɗanda za su kauda hankalin mutane.

Ta wannan dalili ne aka riƙa sa shirye-shirye da za su nishaɗantar da ɗaukacin al'umma, sai dai kash !! Waɗannan shirye-shirye, shiri ne na ƙasashen waje waɗanda suka fi sauƙin sumuwa da aiwatarwa. Samuwar waɗannan shirye-shirye ya haifar da wasu baƙin al'adu ga al'ummar

wannan ƙasa. Wasanni irin su "*Cisco kid*" da "*Hopalong Cassidi*" na gidan Talabijin na Ibadan (WNTV) duk suna cikin irin waɗannan shirye-shiryen.

Yunƙuri na farko na samar da wasan kwaikwayo na 'yan ƙasa shi ne wanda Wole Soyinka ya rubuta mai suna *"My Father's Burden*" wanda gidanTalabijin na Ibadan ya fara yaɗawa a 1960.

Segun O. (1981 :377) ya bayyana samuwar wasu hanyoyi na aiwatar da wasan kwaikwayo ta baddala waɗansu wasanni dandamali da fitatun marubuta irin su Duro Ladipo da J.P Clark zuwa wasannin Talabijin.

Racheal (1986:50) ta ambato Abdurrahman Micika na cewa a 9 ga watan Satumba 1964 ne, aka fara wasan kwaikwayo a gidan Talabijin na Kaduna. Wannan wasa cikin Turanci baddalawar wasan nan na Aldous Huɗlays mai suna "*Gioconda Smile with an All-white cast"*.

Kusan dukkan wasannin farko-farko na NTA Kaduna ana aiwatar da su ne a cikin gidan Talabijin (studio), kuma ana yaɗa su kai tsaye a lokacin da ake aiwatar da su, maimakon a tanaje su tukun, kafin a nuna wa jama'a. Dalilin haka ne ya sa ana iya ganinsu sau ɗaya rak a lokacin da ake aiwatar da su kafin a gama su ɓace, wannan kam ya haifar da rashin samuwar waɗannan wasanni domin gudanar da bincike.

Hukumar gidan Talabijin ta ƙasa (NTA) ta sanya bukin wasan kwaikwayo a 1978. An sami da dama waɗanda an yi ba cikin gidajen Talabijin ba (studio), don yin takara da sauran gidajen Talabijin. Gidajen Talabijin guda goma sha biyu ne suka shiga wannan gasa. Gidan Talabijin na Nijeriya na sakkwato shi ya lashe wannan gasar da wani wasa mai take" Moment of Truth" Wannan wasa na *'Moment of Truth*' ya ci gaba da samun lambar yabo inda ya sami lashe cin kyautar fitattun 'yan wasa a 1983. Ya kuma sami cin wata kyautar ta O.A.U a Aljeriya. Peter Igho ne marubucin wannan wasan, shi ne kuma ya ƙirƙiro wasannan na "Cockcrow at Down" wannan wasa shi ne wasa na farko a gidan Talabijin wanda wata hukumar Banki ta ɗauki nauyin Gudanarwa.

Waɗannan wasannin da suka gabata duk ana aiwatar da su da Turanci ne, ƙasimu Yero ya faɗi cewa: Wasa na farko da aka fara yi a gidan Talabijin na Kaduna na Hausa shi ne, wasan kwaikwayo a 1969 (Hausa Drama) a ƙarƙashin jagorancin Alhaji Abdurrahman Micika. An aiwatar da wasanni masu yawan gaske a ƙarƙashin wannan shiri waɗanda suka shafin al'amuran yau da kullum, misali zaman lafiyar Iyali, da Noma, da Kiwo, da NishaɗI, da kiwon lafiya, da ilimi da tsafta.

Ana cikin wannan wasa ne kuma aka ga ya dace a sami ƙarin wasu wasannin don irin bunƙasar da wasan kwaikwayo na Talabijin yake

samu. ƙare yaƙin Basasa na Nijeriya ya haifar da wasan Samanja a 1972, wasan Samanja wasa ne mai nuna yadda rayuwar da kuma zama irin ta yau da kullum tsakanin Sojoji da kuma farar Hula take. Wasanni huɗu na farko na wannan shirin ƙasimu Yero ne ya ƙirƙiro su kuma ya rubuta su. A wannan wasa na ***"Samanja Mazan Fama"*** ne Usman Baba Fategi yake fitowa a matsayin tsohon Soja mai suna Samanja, shi kuma ƙasimu Yero ya ke fitowa a matsayin farar hula wanda ake masa laƙabi da "Ga maza sai muni" kuma koyaushe suna tare da Samanja.
A waɗannan wasanni, ana ƙoƙarin nunawa jama'a, cewa soja ba abin tsoro ba ne. Kuma ƙoƙarin da wasu ke yi na ɓallewa daga ƙasar ba zai haifar da komi ba illa ɗan da ba ido. Daga baya Usman Baba Fategi shi ya ci gaba da rubuta wannan wasa na Samanja.

Bayan an sami wasanni masu dama a ƙarƙashin wannan shiri na wasan kwaikwayo sai aka sauya masa suna zuwa "Kukan Kurciya" (The Dove Cry). A ƙarƙashin wannan shiri an yi wasanni masu yawan gaske. Ana cikin gudanar da wannan shiri ne kuma a tsakanin shekarar 1975-1978 aka sake sauya masa suna daga "Kukan Kurciya" ya koma "***Tambari***".

Wasan "Tambari" ya samo sunansa ne daga Gangar nan da ake bugawa a Fada mai suna Tambari. Ana buga wannan Gangar ce don isar da saƙo zuwa ga al'umma. Haka ma shirin "Tambari" yake. Domin fadakar da al'umma a kan abubuwan da suka shafi zamantakewa na yau da kullum. Wannan shiri na "Tambari" wanda yake ɗaukan awa ɗaya cur, kusan shi ne wasan kwaikwayo mafi daɗewa (tsawo) da aka aiwatarwa a wannan gidan Talabijin, tare da haɗin gwuiwar cibiyar Nazarin al'adun Gargajiya ta Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya.

Ana cikin waɗannan wasanni ne kuma, sai aka sake ƙirƙiro wani sabon wasa mai suna "***Karambana***" wanda ƙasimu Yero ya ƙirƙira, domin isar da saƙo ga al'umma cikin ban dariya da nisahɗi. A wannan shiri na Karambana ƙasimu Yero ne yake fitowa a matsayin Karambana wato mutum mai karambani a duk inda yake. An yi wasanni da dama a ƙarƙashin wannan shirin waɗanda suke nuni da saƙonni mabambanta irin su gargaɗi da hannunka mai sanda ga waɗansu al'amuran yau da kullum.

Bayan an sami wasanni da dama a ƙarƙashin wannan shiri na "***Karambana***" sai aka yi tunanin ƙirƙiro wani shirin wanda zai ƙunshi raha da kuma gyara ga al'ummar Hausawa. Gwarzon wasan ya kasance dattijo mai faɗa a ji. Sai aka ƙirƙiro shirin "***Baba Cinkisa"***. Shi ma wannan shirin ƙasimu Yero ne ya ƙirƙiro shi a wajen shekarar 1977 - 1978, ana shirya wasan ne a kan abubuwan da suka shafi al'ummar Hausawa ta fuskar al'adunsu, da zamantakewarsu, da tsarin shugabancinsu, da tsaftarsu, da iliminsu.

An zaɓi Dattijo ne ya kasance gwarzon wasan saboda duk inda ya je a cikin wasan ko a Ofis ne ko a gida ko wurin ‘ya’yansa, duk tsawatarwa yake yi a kan abinda yake ganin ya saɓa wa sannannen al’ada ta Hausawa. Su kuma masu yi suna ganin dai-dai ne don ya yi ma son zuciyarsu. Ta haka ne a shirin wasan a kan fito da wasu abubuwa masu yawa waɗanda suka shafi al’ummar Hausawa cikin raha ba tare da an yi wa Baba Cinkisa musu ba. misali an yi wani shiri wanda Kasimu Yero ya je gidan ‘ya’yansa da niyyar ziyara aka kawo masa Salat da soyayyen Dankali da ƙwai, amma don ya nuna ba irin tasa al’adar ke nan ba ta cin tuwo da mai sai ya ambaci cewa wannan ai salon rowa ce da rainin wayo. Ta yaya za a kawo masa waɗannan ganyayyaki abincin ɓeraye a ce ya ci? Da yake ya fito ne a matsayin baba, abinda duk ya yi faɗa a kai ba mai masa musu komin rashin daɗinsa, sai ma in ya fita ne su rinƙa faɗin ka ji Baba da wata irin Magana, ko a halin da ake aiwatar da wannan bincike ana ta ƙoƙarin lallashin ƙasimu Yero kan a dawo da wannan shiri na Baba Cinkisa saboda ganin cewa muna yanayi na mulkin Demokaraɗiyya, kuma akwai buƙatuwar a ilmantar da mutane a kan sanin haƙƙinsu da daina karɓar cin hanci da rashawa wanda ma’aikatan Gwamnati ke yi.

Bayan an yi shekaru da dama ana shirya waɗannan wasanni, sai aka ga ya dace a 1978-1979 a ɗauki wani littafin Ta’alifi na Hausa domin a baddala shi zuwa wasan kwaikwayo, wannan kuwa an yi shi ne domin samar da dama ga jama’ar da ba su iya karatu ba su ma su iya gani a zahiri ɗauke da hoto da sauti. Ƙasimu Yero ne ya ɗauki ɗawainiyar wannan aiki na Baddalawa, kuma da taimakon Allah da gudummowar wasu ‘yan wasa aka iya baddala wannan littafi na Magana Jari ce zuwa wasan kwaikwayo.

Bayan an sami shekaru da dama ana gudanar da wasan kwaikwayo iri-iri, sai kuma aka sake ƙirƙiro wani sabon shirin wasa wanda zai haɗa dukkan muhimman ƙabilu ƙasar nan wuri guda. An shawarci ƙasimu Yero ko a kan yaya za a shirywa wannan wasa ya ce a ba shi kwana ɗaya don ya yi tunani. Ya ga cewa maimakon a ce an zauna a aji da mutane masu yare da yawa gara ya ɗaukin yadda zaman Kaduna yake. Zaman irin ta Zariya da Kano da Katsina duk ta sha bambam da irin zaman Kaduna. Waɗannan wurari a gida guda akan sami mai gida daga shi sai ‘ya’yansa da ‘yan’uwa, amma a zama irin ta Kaduna akan sami gidan haya mai ƙabilu da dama masu al’adu mabanbanta da juna, amma suna zaune a gida ɗaya tamkar dai yadda ƙasar nan tamu Nijeriya ta ke mai ƙabilu da dama.

Saboda haka ne sai aka ƙirƙiro shirin “***Ba Cinya ba ƙafar Baya”*** domin a nuna wa jama’a yadda za su iya zaunawa tare da juna ƙarƙashin ƙasa ɗaya ciki kwanciyar hankali da zaman haƙuri. An yi ƙoƙarin samun

mutum guda wanda zai zama shi ne mai kula da wannan gidan hayan, zai riƙa karɓar kuɗin haya kuma yana rabon faɗa.

An ba da shawarar a sami sojan da ya aje aiki a ba shi wannan muƙami, sai aka ga cewa ba za a kira shi da Samanja ba, domin akwai wani shiri na Samanja, saboda haka aka laƙaba masa suna da "***Kwatamasta".*** ƙasimu Yero shi ya rinƙa rubuta wannan wasa kuna yake fitowa a matsayin mai zaune a wannan gidan haya. A wannan gidan hayan kusan kullum sai an yi rigima tsakanin mazauna wannan gidan, akan wasu dalilai da ba su taka kara sun ƙarya ba. Jami'in mai kula da wannan gida shi ne Kwatamasta. Baya ga karɓar kuɗin haya, a kullum yana cikin yin sulhu da sasantawa ne a tsakanin mazauna wannan gida tare da nuna musu cewa dole ne fa a zauna lafiya tun da Allah ya haɗa zamanasu a wuri guda. Wannan wasa kwatankwacin wanda aka rinƙa yin sa ne da Turanci na **Mind Your Language** an sami wasanni masu ɗan dama ƙarƙashin wannan shirin sai dai bai ɗore ba.

Ana cikin gudanar da wasannin kwaikwayo iri-iri sai a shekara 1984 - 1985 aka sake ganin baƙatuwar a mayar da ko kuma a fassara wasan "Magana Jari ce" daga harshen Hausa zuwa harshen Turanci. An tuntubi ƙasimu Yero kan wannan aiki, nan da nan sai ya amsa da zai iya yi. Da farko wannan aiki an so a aiwatar da shi ne a NTA Kano, to amma ƙasimu Yero ya koka da cewar shi da yake Kaduna ta yaya za a kai shirin NTA Kano, saboda haka nan da nan ya rubuta takardar koke kuma ya nemi wasu 'yan wasa uku suka rattaba hannunsu a kan sun yarda da a bar wannan shiri a NTA Kaduna. Daga ƙarshe aka yarje masa aka bar wannan shiri a NTA Kaduna aka kuma ɗora masa alhakin shiryawa da kuma rubuta wasannin. Hannu ɗaya baya ɗaukar Jinka sai ya nemi haɗin kan sauran 'yan wasa domin kowa ya ba da irin tasa gudummuwar wajen gudanar da gagarumin wannan aiki, kuma Allah da ikon sa wannan aiki ya sami nasara. An fassara waɗannan wasanni na "Magana Jari ce" daga harshen Hausa zuwa harshen Turanci. Ana kiran wasan da suna *Wisdom is an Asset* wannan shi ne ɗan taƙaitaccen tarihin samuwar wasan kwaikwayo a gidan Talabijin na Kaduna.

Auna Fahimta

| |
|---|
| 1- Wane ne rubutaccen wasan kwaikwayon da aka fara ɗauka a matsayin na farko?<br>2- A wacce shekara aka yi wasan kwakwaiyo? |

## 5.6 Taƙaitawa

Wannan gava ta ƙunshi bayanin rubutaccen wasan kwaikwayon Hausa, inda aka bayyana ma'anar rubutaccen wasan kwaikwayo da samuwarsa da ire-irensu, an kuma yi bayanin gudunmuwar da Turawa suka bayar wajen samuwar rubutattun wasannin kwaikwayon Hausa. Sa`annan daga ƙarshe an rarraba wasannin zuwa wasannin farko-farko da na tsakiya kana aka ƙarasa da na kwanan nan.

Ayyukan da ake gabatarwa a gidajen rediyo kuwa waɗanda aka yi wa laƙabi da adabin rediyo, sun ƙunshi shirye-shiryen da ake yin su don manya da matasa da kuma ƙananan yara. Ire-iren waɗannan shirye-shiryen sun haɗa da wasannin yara da kaci-kacici da wasa ƙwaƙwalwa da wasannin kwaikwayon, waɗannan da ma wasu da ba a ambata ba, su ne ayyukan adabin. Sai dai a lura babu mamaki wasu daga cikin su sai da aka samar da su walau ta rubutacciyar hanya ko ta wata hanyar ta daban, matuƙar dai wajen wanzar wa an yi amfani da rediyo, kuma babu inda ake wanzar da wannan aiki in ba rediyon ba, adabin ya zama na rediyo.

A wannan kashi ne kuma, aka yi bayanin abubuwan da suka shafi talbijin tun daga ma`anar adabin talbijin da yadda talbijin ya iso ƙasar Hausa da dalilan da gwamnatin tarayya ta bayar wajen karve gidajen talbijin na yankuna aka maida su ƙarƙashin tarayya. Baya ga nan mun ga yadda wasan kwaikwayon talbijin ya zama mana fitila a matsayin zakaran gwajin dafi na adabin talbijin.

## 5.7 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Kacici-kacici: - hikima ce wadda ta ƙunshi ƙoƙarin gano wani abu ko kuma yadda abu zai kasance ko warware wata matsala.

## 5.8 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Ahmed, U. B. (1985) *Nau'o'in Wasannin Kwaikwayon Hausa.* Cibiyar Nazarin Al'adun Nijeriya. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Aristotle. (1996). *Poetics.* Trans. By Malcon Heath. England, Penguim Books Ltd.

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Crow, B. (1983). *Studing Drama*, Nigeria, Longman.

Ɗangambo, A. (1981). "Rikiɗar Azanci: Siddabarun Salo da Harshe Cikin Tabarƙoƙo Tahmisin Aliyu Ɗansidi". Cikin Yahaya, I.Y da wasu (ed.) Studies in Hausa Language, Literature and Culture. Kano: Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero University.

Ɗangambo, A. (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano: Bayero University.

Ɗangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Conciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). New York: George Braziller.

……………… (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

………………. (1984): *Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph Publishers.

………………… (2009) 'Adabin Hausa da Mazhabobin Tarke na Duniya: Wa Ta Duba?' in Proceedings of the 2nd International Conference on Hausa Studies African and European Perspectives Kano, Bayero University.

Edward, B. T. (1967) "The Science of Culture" Culture and Consciousness: Perspectives in The Social Science. Gloria B. Levitas (ed). George Braziller, New York.

Ewu, Rachael J. (1986) "The politics of Television Drama in Nigeria, a case study of N.T.A Kaduna". Unpublished M.A. Thesis Department of English A.B.U Zaria.

Gusau, S. M. (2006). Tatsuniya (Gatana) : Sigoginta da Hikimominta. Cikin *Mujallar Algaita*, 4,1.

…………….. (2008): *Dabarun Nazarin Adabin Hausa.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

……………… (2008). *Waƙoƙin Baka A Ƙasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu*. Kano; Benchmark Publishers Limited.

………………. (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Century Research and publishing Limited, Kano

Gusau, S.M (2011) *Adabin Hausa a Sauƙaƙe*. Kano: Century Research and publishing Limited.

Ibrahim, M.S (1982) "Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa ta Gargijiya". Kano. Kundin Digiri na Biyu. Sashen

Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero.

Junaidu, I. Da `Yar'aduwa, T.M. (2007): *Harshe Da Adabin Hausa A Kammale.* Ibadan: Spectrum Books Limited.

Kofoworola, E.O. (1978), "A Comparative Analysis of the Development of Drama in KadunaState and in Medieval and Early Renaissance Europe". Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello.

Malumfashi, I. A (1985). "Asali da Bunƙasar Rubutaccen Wasan Kwaikwayo na Hausa" Kundin Digiri na Biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afrika. Jamiar Ahmadu Bello Zariya.

……………………. (1990). "Rubutaccen Wasan Kwaikwayon Hausa Daga 1930- 1990: Sharhi Kan Matsayinsa" Sokoto, *Forum for Language and Culture: Proceeding of the 30th Anniversary of Writen Hausa Drama.*

Malumfashi, M. A. I. (2004). “Ƙagaggun Labaran Hausa: Abin Da Aka Sani Da Wanda Ba A Sani Ba Ta Fuskar Tarihin Adabi”. Maƙalar Da Aka Gabatar, Sashen Harsunan Nijeriya, Usumanu Ɗanfodiyo University, Sokoto.

……………………. (2009). *Adabin Abubakar Imam*. Sakkwato: Garkuwa Publishers.

……………………… (2018). *Labarin Hausa a Rubuce: 1927-2018*. Zaria: Ahmadu
Bello University Press, Limited.

Omar, S. (2013) Fasahar Mazan Jiya: Nazari A Kan Rayuwa Da Waƙoƙin Malam
Mu’azu Haɗeja. Kaduna: Garkuwa Media Services.

Sa’id, B. (1978) “Gudummawar Masu Jihadi Kan Adabin Hausa”. Kundin Digiri na
Biyu, A.B.C/ A.B.U. Kano.

Sambo, A. (2012). ‘Sake Leƙa Rabe-raben Wasan Kwaikwayon Hausa’ in Amfani, (ed) *Champion Of Hausa Cikin Hausa: A Festchrift in Honour of [alhatu Muhammad.* Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Sarvi, S.A. (2007). *Nazarin Waƙen Hausa*. Kano; Samarib Publishers.

Segun, Olusola (1981) “The Advent of Television Drama in Nigeria” in Yemi Ogunbiyi (ed) *Drama and Theatre in Nigeria. A critical Source Book*. Nigerian Magazine Logos.

Shehu, I. (2005). ‘Tasirin Harshe A Wasan Kwaikwayon Jami’ar Jatau Na Albarkawa’
Unpublished M.A Thesis. Department of Nigerian and African Languages. Ahmadu Bello University.

Sulaiman, I. A. (2007). “Raha a wasannin ƙasimu Yero: Tarken wasannin Karambana” Kundin Digiri na biyu, Jami’ar Ahmadu Bello Zariya.

Tsoho, M.Y. (1983). “Waƙeƙeniya”. Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Umar, M.B. (1987) Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph
Gidan Sa'adu Zungur.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company Limited.

Yahaya, I.Y da Muhammad, S. (1978) *Darussa Akan Adabin Hausa.* Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University.

Yahya, A.B. (1987). *Salo Asirin Waƙa*. Kano: FISBAS Media Services.
……………. (2012). "Waƙa: Ma'ana Da Ɗabi'a Da Ginshiƙanta". Cikin Amfani,

## 5.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Su wane suka yi rubutaccen wasan kwaikwayon da aka fara ɗauka a matsayin na farko?

- Dr R.M East da malam Abubakar Imam da masinjar hukumar malam Basankare

2- A wacce shekara aka yi wasan kwakwaiyo?

- A shekarar 1936,